# Ga Shi Yana Zuwa

## *GAME DA WANNAN MUJALLAN*

Akwai ikkilisiyoyi dayawa a chikin duniya, kuma duka suna kirarin gaskantawa da kuma koyar da Litafin Mai Tsarki. Duka suna da koyaswoyin dabam-dabam, sa'anan dukansu suna koyas da wadansu al'adu.

Tarrayar Ikkilisiyoyin duniya da sauran kungiyoyin ikkilisiyoyi suna ta aiki shekara da shekarak domin su hada kan ikkilisiyoyi bisa ga koyaswoyin da akwai yarda tsakaninsu. Kuma yanzu wanna kokarin bai kai ga nasara ba.

Wannan karamar mujallar a hannunka tana bada koyaswoyin Litafi Mai-Tsarki bisa ga wadansu muhimman kawuna game da rayuwan kirista. Ta kuma kunshi binciken annabci na al'amuran masu zuwa. Annabcin Litafin Ruya ta Yohanna 13:11-18 ya fada mana cewa kasar Amirka zata taso kamar kassa mai cikaken yanci-kasan jama'arta, wanda su suka kafa, dominsu kuma-ikkilisiya mara shugaba (kamar Papa Roma), kuma gwamnati mara sarki: amma, kash, da zata yi Magana da muryar dragon. Ta wurin sadarwa da ruhohi da kuma koyaswoyin karya, za a yaudari jama'a domin su gaskanta karya, cewa Allah ya canja ranar sujada daga assabar, rana ta bakwai ga mako,zuwa lahadi, rana ta fari ga mako. Za a bukaci majalisun dokoki su canja tsarin mulkin Amirka. Za a kafa dokokin kiyaye lahadi, kuma hukuncin zai kasance cin tara da farko, sa'anan zaman kurkuku, sa'anan kuma hukuncin kisa. Litafi Mai Tsarki ya kira wannan SHAIDAN BISAN. Kowace kasa a fuskar duniya nan za su zartas da wadannan dokokin.

Hargisi da dukan zamanu yana kusantowa da sauri, kuma kamar barawo da dare za ta ba duniya mamaki. Dukan duniya zata kasu kashi biyu kawai , masu kiyaye-assabbar da masu kiyaye lahadi.

Mai karatu, manufan wannan yar mujallar shine ya taimake ka daukan kuduri na kwarai, a wanna rayuwa, domin ya shirya ka ga rai na har abada mai zuwa tawurin zuwan Ubangijinmu Yesu Kristi na biyu.



"Ga shi, yana zuwa tare da gajamarai, kowane ido kuma za ya gan shi"
Ruya ta Yohanna 1:7

## *Amfanin binciken Litafin Mai-Tsarki*

Litafi Mai-Tsarki da kanta tana da hujja game da asalinta daga wurin Allah. Banda ita babu wani litafi wanda zata iya badda amsar tambayoyi na zuciya ko kosadda muradunta. Tana danganta kanta da kowace zamani da kowace yanayi na rayuwa, sa'annan cika ta ke da sanin da ke wayadda zuciya yana kuma sarkake rai.

A cikin Litafi Mai-Tsarki, akwai cikaken bayani game da Allah mai-rai. Idan an karbe ta tawurin bangaskiya, tana da ikon canja rayuwa.cikin dukan tarihinta, hannu mai-iko na Allah yana biye da ita, ya kuma kiyaye ta domin rama'an duniya.

Ta wurin haka ne duniyan, da aka tanada mata kalmar Allah, shiryaye domin baza sakon bishara na karshe zuwa ga yan adam, karshen mulkin zunubi, da kuma zuwan Ubangiji cikin daraja. ''wannan bishara kuwa ta mulkin za a yi wa'azinta cikin iyakar duniya domin shaida ga dukan al'umai, sa'anan matuka za ta zo" Matta 24:14.

Kamar jagorar, Litafi Mai-Tsarki ba ta da na buyi. Tana bada salama a cikin gaskantawa, da kuma karfafiyar bege ta nan gaba. Tana magance manyan damuwoyin rayuwa da na makonar mutuwa, tana kuma karfafa tsarkakiyar rayuwa, hakuri, da aikata daidai. Tana cika zuciya da kauna zuwa ga Allah da kuma muradin aikata nagarta zuwa ga wadansu, a wannan hanya kuma tana sa shiri domin rayuwa mai muhimminci a nan domin gida a sama. Tana koyar da tammanin rai ta wurin bayyann abin da aka biya domin fansarta. Ta sanadda abin da shi ne kawai maganin zunubi, ta kuma gabatar mana tsarin dokokin ruhaniya da sune kawai cikakku da aka taba bayarwa. Ta yi Magana game da nan gaba da kuma yanda za a tinkare ta. Tana sa mu kasancewa da gabagadin tsaya ma gaskiya, tana kiyaye ruhaniya cikin kunci da wahala.

**Litafi Mai-Tsarki na da amfani don menene?**

''kowane nassi hurarre daga wurin Allah mai-amfani ne ga kayaswa, ga sautawa, ga kwabewa, ga foro kuma da ke cikin adalci." 1 Timmothawus 3:16.

**Wane shiri ne Allah ke sammanin cimma ta wurin ba da Litafi Mai-Tsarki?**

''Domin mutamin Allah shi zama kamili, shiryaye sarai domin kowane managarcin aiki."aya 17.

**Wane irin sujada ne yakan zama sakamako koyaswoyin karya?**

''amma banza suke yi mani sujada, koyaswadasuke yi dokokin mutane ne" Matta 15:9.

**Wanene ya motsa mutanen da suka yi Magana a madadin Allah?**

''Gama ba a taba kawo kowani anabci bisa ga nufin mutum ba: amma mutane suka yi Magana daga wurin Allah, Ruhu Mai-Tsarki ne yana motsa su" 1Bitrus 1:21.

**Menene dalilin rubuta Litafi Mai-Tsarki?**

''Gama iyakar abinda aka rubuta a da aka rubuta su domin koyaswarmu, domin tawurin hakuri da ta'aziyar litattafai mu zama da bege" Romawa 15:4.

**Menene Kristi ya fada game da binciken Litafi Mai-Tsarki?**

''Kuna binciken litattafai, domin kuna tsamani a cikinsu kuna da rai na har abada, sune fa suna shaidata." Yohanna 5:39.

**Yaya ne kafuwar bangaskiyar anabci Ishaya cikin kalmar Allah?**

''Ciyawa ta kan yi yaushi, fure shi yankwane, amma maganar Ubangiji za ta tsaya har abada." Ishaya 40:8.

**Wane babban albarka ne Krista ya sa bisa almajiransa bayan tashinsa daga matattu?**

''Daga nan ya bude hankalinsu, domin su fahinci litattafai." Luka 24:45.

## *Iko Cikin Kalmar Allah*

**Yaya ne Yesu ya tsauta ma wadanda, ko da shike suna sune da kalmomin Litafi Mai-Tsarki, sun kasa fahintarsu?**

''Amma Yesu ya amsa ya ce masu, kun kuskure don rashin sanin litattafai da ikon Allah." Matta 22:29.

**Wadannene Yesu ya kira masu albarka?**

''Amma ya ce, gwamma dai (masu-albarka ne) wadannan da suna jin maganar Allah suna kiyaye ta kuma." Luka 11:28.

**Ta wurin wadanne koyaswoyi ne za a yaudari wadansu a kwanakin karshe?**

''Amma Ruhu yana fadi a sarari, cikin kwanaki na karshe, wadansu zasu ridda daga imani, suna maida hankali ga ruhohi na rudami da koyaswar aljanu." 1 Timothawus 4:1,2 Bitrus 2:1.

**Zuwa ga menene mutane zasu karkata kunnuwarsu?**

''Gama kwanaki zasu zo inda ba za su daure da koyaswa mai lafiya ba; amma bisa ga kaikayin kunnuwa za su tattara wa kansu masu-koyaswa bisa ga sha'awoyinsu; za su kawasda

kunuwansu ga barin gaskiya, su karkata zuwa wajen tatsuniyoyi." 2 Timothawus 5:21.

**Menene Litafi Mai-Tsarki yana da iko yi ma wanda ya gaskanta shi?**

''Tun kana jariri fa ka san litattafai masu-tsarki wadanda ke da iko su hikimtadda kai zuwa ceto ta wurin bangaskiya wanda ke cikin Kristi Yesu."2 Timothawus3:15.

**Ta wurin menene zamu sami tsarkakewa?**

''Ka tsarkake su cikin gaskiya; maganarka ita ce gaskiya." Yohanna 17:17

**Wadanne ne almajiran Yesu, kuma wane aikin alheri ne gaskiyan tana yi ma wadanda suka karbe ta?**

''Yesu ya ce ma wadannan yahudawa da suka bada gaskiya gareshi, idan kun zamna cikin maganata, kune almajiraina na gaske; ku a san gaskiya kuma, gaskiya kuwa zata yantasda ku."Yohanna 8:31-32.

**Yaya ne zamu iya kwatanta halin kalmar Allah?**

''Gama maganar Allah mai-rai ce mai alkatawa, ta fi kowane takobi mai kaifi biyu ci, tana kuwa hudawa har zuwa rarrabon rai da ruhu, da gababuwa da bargo kuma, tana kuwa da hanzari ga ganewar tunanin zuciya da nufe-nufenta." Ibraniyawa 4:12.

**Ta warin menene masu-bi suna tsabtatuwa?**

''Ko yanzu ku tsarkakakku ne saboda magana da na fada maku" Yohanna 15:3.

**Ta yaya ne saurayi ya kan iya tsabtata al'amuransa?**

''Da me samari za ya tsarkake al'amuransa? Sai ta wurin tsare wassu bisa ga maganarka." Zabura 119:9.

## *Muhummincin Adu'a*

**Yayane mai-zabura ya kan fuskanci Allah?**

''Ya mai jin adu'a, a gareka dukan masu-rai zasu zo." Zabura 65:2.

**Bisa wadanne sharuda ne an yi mana alkawuran albarkun da muke bukata?**

''Ku roka za a baku;ku nema za ku samu; ku kwankwasa za a bude maku; gama dukan wanda ya ke roka yana karba; wadanda ke nema kuma yana samuwa; wadanda ke kwankwasawa kuma za a bude masa." Matta 7:7-8.

**KA LURA**: Adu'a bude zuciya ne ga Allah kamar ga aboki; Adu'a bay a canja Allah. Yana ajiye mu a hanyar albarka, da kuma cikin tunanin cewa Allah zai amsa rokonmu bisa ga bukatunmu.

**Bisa ga wane sharadi ne mai zabura ya ce Ubangiji ba zai amsa adu'a ba?**

''Idan na kiyaye mugunta cikin zuciyata, Ubangiji ba za ya ji ba."Zabura 66:18. duba Ishaya 59:1-2, Yakubu 4:3

**Adu'an wanene Solomon y ace abin kyama ne?**

''Wanda ya kawasda kunnensa daga jin shari'a, ko addu'atasa abin kyama ne." Misalai 28:9.

**Domin wanene Kristi ya koyas mana mu yi addu'a?**

''Amma ni in ace maku, ku yi kaunar magabtarku, kuma wadanda kan tsananta maku, ku yi masu addu'a." Matta 5:44.

**Ta yaya za mu tsare ma jaraba?**

''Ku yi tsaro, ku yi addu'a, kada ku shiga cikin jaraba:ruhu lallai ya yarda amma jiki rarauna ne." Matta 26:41

**Yaya ne ya kamata dole mutum ya roka domin ya karba?**

''Amma bari shi yi rook da bangaskiya, bad a shakka komi ba:gama maishakka yana kama da rakumin teku, wanda iska yana karassa, yana jijjigassa kuma ."Yakubu 1:6-7. duba Markus 11:24.

**Ka LURA:** Addu'a mabudi ne cikin hannu na bangaskiya domin bude ma'ajin sama, inda ikon Allahntaka mara iyaka ke ajiye.

**Zuwa ga menene aka galgademu mu yi tsaro?**

''Amma matukar dukan abu ta kusa: domin wannan ku yi natsuwa cikin hankalinku, ku yi rai shimfida zuwa ga addau'a." 1 Bitrus 4:7.

**Yaya yawan yanda ya kamata mu yi adda'a?**

''Ku yi addua'a ba fasawa."1 Tassalonikawa 5:17, ''kuna lizima cikin addu'a." Romawa 12:12.

## *Halita Da Mahalici*

**Wanene ya halici sama da kasa?**

''A cikin farko Allah ya halitta sama da kasa." Farawa 1:1.

**Menene Allah ya yi amfani da shi a halittan sama da duniya?**

''Da maganar Ubangiji aka yi samai, Rundunansu duka kuma da lumfashin bakinsa." Zabura 33:6-9.

**Ta wurin wanene Allah ya halicci abu duka?**

''Gama a cikinsa (dukan mutum) aka halice dukan abu, cikin sammai da bisa duniya kuma abubuwa masu-ganuwa da abubuwa marasa ganuwa, ko kursiyai, ko tsarautai ko mulkoki ko ikoki;dukan abu ta wurinsa an halitta su dominsa kuma." Kolosiyawa 1:16,Yohanna 1:3. duba Ibraniyawa 1:1-2.

**Menene manufan Allah don halittan duniya?**

''Gama hakanan Ubangiji ya fadi, shi wanda ya halici sammai; shi ne Allah; mai-sifinta duniya mai-yinta kuma; shi ya kafa ta, ya halice ta ba wofi ba, ya kamata ta domin wurin zama; ni ne Ubangiji, babu wani kuma ."ISHAYA 45:18

**Yaya ne Allah ya tanada mazamna duniya da ya halitta?**

''Ubangiji Allah kuwa ya sifinta mutum daga turbayar kasa, ya hura masa lumfasin rai cikin halinsa, mutum kuma ya zama rayayyen mai-rai." Farawa 2:7.

**Cikin suran wanene aka halicci mutum?**

''Allah fa ya halitta mutum cikin suratasa, cikin surar Allah ya halicci shi, na miji da ta mata ya halice su." Farawa 1:27.

**An halicci dukan abu tawurin Kristi ne?**

''Gama a cikinsa (Dan mutum) aka halitta dukan abu, cikin sammai da bisa duniya kuma, abubuwa masu-ganuwa da abubuwa marasaganuwa, ko kursiyai ko sarautai ko mulkoki ko ikoki, ta wurinsa an halitta su, dominsa kuma, shi ne kuwa gaba da dukan abu, a cikinsa kuwa dukan abu suna harhade. Shi ne kuma kai na jiki, watau ekklisiya; mafari ne haifan fari daga cikin matattu; domin cikin dukan abu shi zama magabaci." Kolosiyawa 1:16-18.

**Wane nasi ne ya nuna a fili cewa ikon halitta ne ke canja rayuwar mai-bi?**

''Gama mu kirassa ne, halittattu cikin Kristi Yesu zuwa kyawawan ayuka, wadanda

Allah ya rigaya ya shirya da za mu yi tafiya a cikinsu ."afisawa 2:10.

## *Asalin (Tushin) Mgunta*

**Yaya ne an kwatanta gwaggwarmaya tsakanin Kristi da Shaitan?**

''Aka yi yaki cikin sama;Mikailu da nasa malaiku suna fita suyi gaba da dragon; dragon kuma yayi gaba tare da nasa malaiku; ba su rinjaya ba, ba a kwa kara tarasda matsayinsu cikin sama ba. Aka jefasda babban dragon, tsofon macijin, shi wanda ana ce da shi Ibilis da Shaitan, mai-rudin dukan duniya; aka jefasda shi a duniya, aka jefsada malaikunsa kuma tare da shi ." Ruya ta Yohanna 12:7-9

**KA LURA:**Wannan gwaggwarmayan ya sami asali daga sama ne kuma ya ci gaba a cikin duniya.

**Zunubi ta samo asali daga wurin wanene?**

''Wanda ya ke aikata zunubi na Shaitan ne; gama Shaitan yana yin zunubi tun daga farko." 1 Yohanna 3:8

**Tun daga wane lokaci ne Shaitan ya kasance mai-kisan kai?**

''Ku na ubanku Shaitan ne, kyashe kyashe na ubanku kuna da nufi kuyi. Shi mai-kisan kai ne tun daga farko, ba ya tsaya a kan gaskiya ba, domin babu gaskiya a cikinsa." Yohanna 8:44.

**Shaitan da ma asalinsa mai zunubi ne shi?**

''Tun randa aka halice ka kamiltace ne kai a cikin dukan al'amurnaka, har randa aka iske rashin gaskiya (zunubi) a cikinka." Ezekiel 28:15.

Kalamin nan na cikin Yohanna 8:44 da ya ce ba ya "tsaya a kan gaskiya ba", ya nuna cewa Shaitan asalinsa kamili ne, kuma ya taba kasancewa cikin gaskiya. Bitrus ya yi Magana game da ''malaiku sa'anda suka yi zunubi" (2 Bitrus 2:4); kuma Yahuda ya ja hankalinmu zuwa ga malaiku ''wadanda ba su rike masayi nasu ba." Yahuda 6. Wadannan malaikun ma sun taba kasancewa cikin rashin zunubi.

**Wadanne Karin kalamai ne na Kristi kuma sun kara dora alhakin asalin zunubi bisa Shaitan da malaikunsa?**

''Sa'annan za ya ce ma wadanda ke ga hannun hagunsa," ku rabu da ni ku la'antattu, zuwa cikin wuta ta har abada, wanda an shirya ma Shaitan da malaikunsa." Matta 25:41

## *An Bambanta Kristi Da Shaitan*

**Menene ya kai ga zunubi, tawaye, da kuma faduwar Shaitan?**

''Zuciyarka ta daukaka saboda jamalinka; hasken ranka ya bata hikimarka." Ezekiel 28:17

''cikin zuciyarka ka ce," har sama zan hau, zan daukaka kursiyina bisa tamrarin Allah; zan zamna bisa dutse na taron jama'a, can kurewar arewa….in maida kaina kamar Mai-iko duka." Ishaya 14:13-14

**Menene ya sa a lokaci daya an furta kaito a bisa duniya?**

''Domin wanna fa, ku yi farinciki ya sammai, da ku mazamna a ciki. Kaiton

duniya da teku; domin ya sani sauran zarafinsa kadan ne."Ruya ta Yohanna 12:12.

''Na gan shaitan fadade kamar walkiya daga sama ''Luka 10:18.

## *Faduwar Mutum*

**Yaushe ne zunubi da mutuwa sun shigo duniya nan?**

''Domin wannan fa, kamar zunubi ya shigo cikin duniya ta wurin mutum daya(Adamu), mutuwa kwa ta wurin zunubi; har fa mutuwa ta bi kan dukan mutane, da shike dukan sun yi zunubi." Romawa 5:12

**Da wadanne kalmomi ne Allah ya sharanta Ka'inu kamar mai zunubi?**

''Idan ka kyauta, ba za a amsa ba? Idan kwa ba ka kyauta ba, zunubi yana kwance a bakin kofa…. Sai (Allah) ya ce, me ka yi? Muryar jikin kaninka ta yi kara a wurina daga kasa. Yanzu fa la'antace ne kai daga kasa, wanda ta bude bakinta karbi jinin kaninka daga hannunka"Farawa 4:7-11.

**Wane Karin la'ana ne sakamakon kisan kai na farkon ya haifar?**

''Sa'anan ka yi noma, kasa baza ta kara baka karfinta ba." Farawa 4:12.

**Yaya ne zunubin Adamu ya shafi duniyan kanta da kuma halitta na itatuwa da ciyayi?**

''sabili da kai na la'anta kasa; da wahala za ta haifi maka; ganyen saura kuma za ka ci." Faraway 3:17-18.

**Menene hakin zunubi?**

''Hakin zunubi mutuwa ne." Romawa 6:23. ''Cikin rana da kaci, mutuwa za ka yi lallai."Farawa 2:17. ''Mai-rai da ya yi zunubi shi za ya mutu"Ezekiel 18:4.

**Yaya ne mutum zai guje ma wannan hukuncin?**

''Gama haikin zunubi mutuwa ne; amma kyautar Allah rai na har abada che chikin Kristi Yesu Ubangijinmu." Rimawa 6A:23.

**Menene zunubi?**

" Dukan wanda yake aika zunubi ya ketare shari'a kuma; zunubi shi ne ketaren shari'a" 1 Yohanna 3:4.

**Menene ya kan faru kafin bayanuwan zunubi?**

''Sa'anan lokacinda sha'awa ta habaka, ta kan haifi zunubi."Yakubu 1:15. ''Iyakar abinda ba na bangaskiya bane zunubi ne" Romawa 14:23.

**KA LURA ;** mu kan ketare dokoki ko kin yin biyaya ga Allah ta wurin rashin dangana ga kuma rashin bangaskiya gare shi.

## *Sakamakon Zunubi*

**Menen sakamako na karshe, ko abinda zunubi ya kan haifar?**

''Zunubi kwa, sa'anda ya kasaita, ya kan haifi mutuwa." Yakubu 1:15

## *Bukatan Mai-Ceto*

**Zuwa ga wanene an bada wannan kyautan?**

''Gama Allah ya yi kaunar duniya har ya bada Dansa haifeffe shi kadai domin dukan wanda yana bada gaskiya gareshi kada ya lallace amma ya sami rai na har abada." Yohanna 3:16.

**Yaya ne ake karban wannan kyautan?**

''Wanda yana bada gaskiya gerishi ba a yi masa shari'a ba; wanda ba ya bada gaskiya gareshi ba an rigaya an yi masa shari'a, domin ba ya bada gaskiya ga sunan Da haifeffe kadai na Allah ba." Yohanna 3:18. ''Amma iyakar wadanda suka karbe shi ya basu iko su zama yayan Allah, watau wadanda suka bada gaskiya ga sunansa." Yohanna 1:12.

## *Menene Zunubi?*

**Yaya ne Littafi Mai-Tsarki ya kamanta shi?**

''Dukan wanda ya ke aika zunubi yana ketere shari'a kuma; zunubi shine ketaren shari'a. kun sani aka bayana shi domin daukan zunubi; a cikinsa kwa babu zunubi." 1 Yohanna 3:4-5.

**Menene sakamakon zunubi ta ganganci?**

''Gama idan muna yin zunubi da nufin zuciyarmu bayanda mun karbi sanin gaskiya, babu sauran wata hadaya domin zunubai, sai sauraro mai-ban tsoro ga shari'a, da zafin wuta wanda za ta cinye magabta." Ibraniyawa 10:26-27. duba kuma aya 28,29.

## *Dokokin Allah*

**Yaya ne Allah ya sanarda dokokinsa ga mutanensa?**

''Daga cikin tsakiyar wuta kwa Ubangiji ya yi Magana da kai; kuka ji muryar zantattuka, amma ba ku ga wata sura ba; sai murya ya kuma habarta maku alkawalinsa, wanda ya umurce ku ku cika, watau su dokoki gomadin nan, ya kuma rubuta su a cikin alluna guda biyu na dutse" Kubawar Shari'a 4:12-13. Duba kuma Nehemiah 9:13-14. Game da dokoki gomadin, duba Filibiyawa 20:1-17.

**Yaya ne an fasara dokokin ga ganewanmu?**

''Ji tsoron Allah ka kiyaye dokokinsa, gama wannan kadai ne wajibin mutum," Mai-wa'azi 12:13

**Menene halin dokokin Allah ?**

''Hakanan ya fa shari'a tsatsarka ce, doka kuma tsatsarka ce, mai-adilci kwa, tagari ce… gama mun sani shari'a mai-ruhaniya ce; amma ni ba-jiki ne, sayayye ne kalkashin zunubi." Romawa 7:12,14.

**Menene ya nuna cewa dokoki gomadin, wadanda aka furta su, aka kuma rubuta su a dutsen Sinai, dokokin yanci ne ga Krista?**

''Gama iyakar wanda ya kiyaye dukan shari'a (dokokin), amma ya yi tuntube a cikin daya, ya zama mai-laifi ga duka. Gama shi wanda ya ce, ba za ka yi zina ba, ya ce kuma,ba za ka yi kisankai ba. Idan fa ba ka yi zina, amma ka yi kisankai, ka zama mai-ketaren shari'a. Haka za ku yi Magana, haka za ku aika kuma, kamar mutane wadanda za a yi masu shari'a bisa ga shari'a ta yanci," Yakubu 2:10-12.

**Ko mutum zai iya sanin Allah ba tare da kiyayye dokokinsa ba?**

''Wanda ya ce, na san shi,amma ba ya kiyaye dokokinsa ba, makaryaci ne, gaskiya kwa ba ta cikinsa ba." 1 Yohanna 2:4.

**Yaya zamu san cewa muna kaunar yan'uwarmu?**

''Inda mun sani muna kaunar yayan Allah ke nan, lokacinda muna kaunar Allah, muna aikata dokokinsa kuma." 1 Yohanna 5:2.

**Menene kaunar Allah?**

''Gama kaunar Allah ke nan mu kiyaye dokokinsa; dokokinsa fa ba su da ban ciwo ba." Aya 3.

**Wane hali ne Kristi ya nuna ga dokokin Ubansa?**

''Na kiyaye dokokin Ubana, ina zamne kuma cikin kaunatasa." Yohanna 15:10.

**Idan wani yana kirarin kasancewa cikin Kristi, yaya ne ya kamata yayi tafiya?**

''Wanda ya ce yana zamne cikinsa , ya kamata shi da kansa yayi tafiya kamar yadda shi ya yi tafiya." 1Yohanna 2:6.

**Menene Yesu ya fada game da halinsa zuwa ga dokokin?**

''Kada ku zace na zo domin in warware Attaurat da Annabawa; ban zo domin in warware ba, amma domin in cicika." Matta 5:17.

**Menene ya koyas game da tabbatuwar dokokin?**

''Gaskiya fa ni ke fada maku, har sama da duniya su shude, ko wasali daga ko digo daya ba ya shude daga Attaurat ba, sai dukan abu ya cika." Aya 18.

**Wane irin muhimminci ne Allah yana duban rayuwan Krista da shi?**

''Gama iyakar wanda ya kiyaye dukan shari'a; amma ya yi tuntube a cikin daya, ya zama mai-laifi ga duka." Yakubu 2:10.

## *Dokokin Da Bishara*

**Menene manufan dokokin?**

'Gama tawurin ayukan shari'a babu mai-rai da za shi barata a gabansa ba; gama ta wurin shari'a a ke sanin zunubi." Romawa 3:20.

**Menene aka ce shine bishara?**

''Gama bishara ba abin kunya ba ce a gareni; gama ikon Allah ce zuwa ceto ga kowane mai-bada gaskiya." Romawa 1:16.

**Menene Kristi ya alkawarta game da sabon alkawalin?**

' Amma yanzu ya amshi hidima wanda ta dara, da shike kuma shi masakanci ne na mafificin alkawali…gama wannan shine alkawali da zan yi da gidan Isra'ila. Bayan wadannan kwanaki, in ji Ubangiji; in sa dokokina a cikin hankalinsu.bisa zuciyarsu kuma zan rubuta su." Ibraniyawa 8:6, 10.

**Don menene zuciyar mutum ba-jiki yana gaba da Allah?**

" Domin himmatuwar jiki gaba ce da Allah. Gama ba ta cikin biyayya ga shari'ar Allah ba, ba ta iya kwa." Romawa 8:7

**Ko mutum, da karfin kansa, ya kan iya kiyaye dokokin ba tare da taimakon Kristi ba?**

"Nine kuringar anab, kune ressan; wanda yake zamne cikina, ni kuma cikinsa, wannan yana bada yaya dayawa: gama in ba tare da ni ba, ba ku iya yin komi ba." Yohanna 15:5. Duba Romawa 7:14-19.

**Menene Yesu ya ce zai shiga mulkin sama?**

"Ba dukan mai-ce mani, Ubangiji,Ubangiji, za ya shiga cikin mulkin sama ba, sai wanda ke aikata nufin Ubana wanda ke cikin sama."Matta 7:21.

**Yaya ne za a kwatanta mutane bisa ga dangantakansu da dokoki gomadin?**

"Dukan fa wanda ya ketare guda daya ma-fi karamta daga cikin dokokin nan, har ya koya ma mutane haka, za a ce da shi ma-fi karamta a cikin mulkin sama: amma dukan wanda za ya aikata su har ma ya sanas, za a ce da shi mai-

girma a cikin mulkin sama." Matta 5:19.

**Ko mai-bi zai iya cin gaba a cikin zunubi bayan wannan?**

"Me za mu ce fa? Za mu lizima cikin zunubi domin alheri shi yawaita? Daidai! Mu da muka mutu ga zunubi, ka ka za mu kara rayuwa a ciki? Romawa 6:1,2.

**Wace nasi ce ta kawasda dukan begen samun barata ta wurin ayukanmu?**

" Gama ta wurin shari'a ba mai-rai da za shi barata a gabansa ba; gama ta wurin shari'a a ke sanin zunubi." Romawa 3:22.

**Ta wace hanya ce dukan masu-bada gaskiya ga Kristi su ke samun barata?**

"Bisa ga alherinsa, an barata a yawalce ta wurin fansa da ke cikin Kristi Yesu." Aya 24

**Wace fasara ta ruhaniya ce Kristi ya yi ma doka na shidda da na bakwai?**

"Kun ji aka fada ma mutane da; ba za ka yi kisankai ba; da kuma kowanene ya yi kisankai ya shiga hatsarin hukunci; amma ina ce maku, kowanene ya yi fushi da dan'uwansa ya shiga hatsarin hukunci." Matta 5:21,22.

"Kun ji aka fada, ba za ka yi zina ba: amma ina ce maku, dukan wanda ya duba mace har ya yi kyashinta, ya rigaya ya yi zina da ita cikin zuciyarsa." Aya 27-28.

## *Wahalolin Kristi*

**Menene annabci ya ce Kristi zai jimre?**

" Aka wulakance shi,duk da haka ya yi tawali'u, ba ya bude bakinsa ba; kamar dan rago da a ke kai wurin yanka, kamar tumakiya wurin masu-sosayanta tana shuru; hakanan ba ya bude bakinsa ba. Bisa ga rashin gaskiya a shari'a aka kawasda shi: don mutanen zamaninsa fa, wanene a cikinsu ya lura aka datse shi daga kasar masu-rai ? Sabili da laifofin mutanena aka buga shi." Ishaya 53:7,8.

**Ko Kristi da ya san abinda zai fuskamta?**

" Ya dauko su gama sha biyu, ya ce masu, ga shi, za mu tafi Urishalima, za a yi masa ba'a da wulakanci kuma, za a tofa masa miyau: za su yi masa bulala, su kasha shi; rana ta uku kuma za ya tashi." Luka 18:31-33.

**Wane irin tsananci mai-ban kunya ne Kristi ya sha daga hannun masu-tsaro(sojoji)?**

" Suka tubka rawani na kaya, suka sa masa a kai, suka sa gora cikin hannun damansa; "a gaishe ka", suna ta yi masa ba'a, suna cewa "kai,Tsarkin Yahudawa", suka tofa masa miyau, suka karbi goran, suka buge shi a kai." Matta 27:29-30.

**Bayan da aka kawo shi wurin sa aka giciye shi, menene aka ba shi domin a sa shi maye(buguwa)?**

"Suka ba shi ruwan anab garwaye da ruwan matsarmama, domin shi sha: amma sa'anda ya dandana, ya ki sha." Aya 34.

**A wane addu'a ne domin wadanda suka giciye shi Kristi ya bayana ainihin ruhun bisharan-kauna zuwa ga masu-zunubi?**

"Yesu ya ce,Uba,ka yi masu gafara; gama ba su san abinda suke yi ba." Luka 23"34.

**Da wadanne kalmomi ne manyan malamai da sauran jama'a suka yi ma Yesu ba'a a kan giciye?**

"Hakannan kuma manyan malamai suna yi masa ba'a, tare da marubuta da datibai, suka ce "ya ceci wadansu,ya kasa ceton kansa. Tsarkin Isra'ila ne shi; sabko yanzu daga giciye, mu kwa mu a bada gaskiya gareshi."Matta 27:41-42.

**Menene ya fara a karshen wannan abin ban takaicin?**

" Yesu fa, sa'anda ya karbi ruwan tsami, ya ce, ya kare: ya sunkuyadda kansa, ya saki ransa" Yohanna 19:30.

## *Tashin Kristi Daga Matattu*

**"Ni ne Mai-rai; na mutu, ga shi kwa, ina da rai har abada, ina kwa da makulai na mutuwa da** na kabari." Ruya ta Yohanna 19:30.

**Bayan tashinsa daga matattu, wane tasiri ne wannan kalami ya kasance da shi a kan almajiransa?**

"Sa'anda aka tashe shi daga matattu, almajiransa suka tuna ya fadi wannan: suka gaskanta Litattafai da Magana wanda Yesu ya fadi kuma." Yohanna 2:22.

"Gama na bayas gareku tun dafari abin da ni kuma na karba, Kristi ya mutu domin zunubanmu bisa ga litattafai, aka bizne shi; aka tashe shi kuma rana ta uku bisa ga litattafai" 1 Korintiyawa 15:3-4.

"Ya bayana ga Kefas; kana ga su goma sha biyu; daga baya ya bayana ga wadansu yan'uwa, sun yi hamsaminya, baki daya, a cikinsu fa yawansu sun wazu har wa yau, amma wadansu sun rigaya sun yi barci; haka ya bayana ga Yakubu; haka ga dukan manzanni." Aya 5-7.

## *Barata Ta Wurin Bangaskiya*

**Yaya ne Allah ya kan baratar da mutum?**

"Domin mu, baratattu bisa ga alherinsa, mu zama magada bisa ga begen rain a har abada." Titus 3:7.

**Ta wane hanya ne mai-zunubi yana samun wannan alheri mai barataswa?**

"Balle fa yanzu, baratattu ne ta wurin jininsa (Kristi), za mu tsira daga fushin Allah ta wurinsa." Romawa 5:9

**Yaya ne ana iya karban wannan barataswan?**

"Mun aza fa mutum ta wurin bangaskiya ya ke barata banda ayukan shari'a." Romawa 3:28.

**Ta wace hanya daya ce kadai masu-zunubi suna iya barata ko kasancewa adilai?**

"Amma mun sani mutum ba za shi baratta bisa ga ayukan shari'a ba, sai ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kristi, mu da kanmu muka bada gaskiya ga Kristi Yesu, domin mu barata ta wurin bangaskiya cikin Kristi; ba bisa ga ayukan shari'a ba: gama bisa ga ayukan shari'a ba mai-rai da za shi barata." Galantiyawa 2:16.

**Ta yaya ne barataswa ga mai-zunubi ba shi yiyuwa?**

"Gama ta wurin ayukan shari'a ba mai-rai da za shi barata a gabansa ba: gama ta wurin shari'a ake sanin zunubi." Romawa 3:20.

**Yaya ne mutuwan Krsiti ya shaida wannan?**

"Ni ban banzarta alherin Allah ba: gama idan adilci ta wurin shari'a ya ke, Kristi ya mutu banza kenan." Galantiyawa 2:21.

**Menene sakamakon duk wani kokarin da a kan yi domin samun barata ta wurin shari'a (kiyaye doka kadai)?**

"Ba ruwanku da Kristi, ku da ku ke so ku barata ta wurin shari'a: kun bace daga alheri." Galantiyawa 5:4.

**Don menene Isra'ilawa sun kasa kai ga adalci?**

"Amma Isra'ila, cikin bin shari'a adalci , ba su nuski shari'an (adalcin) nan ba. Suka yi tuntube wajen dutsen tuntubewa." Romawa 9:31-32.

**Menene shari'a ke bayanawa?**

"Ta wurin shari'a ake sanin zunubi." Romawa 3:20.

**Menene shaidan adilci na gaskiya wanda ake samu ta wurin bangaskiya, ba ta wurin ayukan shari'a ba?**

"Amma yanzu banda shari'a wani adilci na Allah ya bayana Attaurat da Annabawakwa suna shaidassa." Aya 21.

**Yaya ne yawa bukatan bangaskiya?**

"Ba shi kwa yiyuwa a gamshe shi(Allah) ba sai tare da bangaskiya." Ibraniyawa 11:6.

**Wace nassi ce ta nuna cewa adilci da ke samuwa bisa ga alheri ta wurin bangskiya kada ya zama hujjan cin gaba cikin zunubi?**

"Me za mu ce fa? Za mu lizima cikin zunubi domin alheri shi yawaita? Daidai! Mu da muka mutu ga zunubi, kaka zamu kara rayuwa a ciki?." Romawa 6:1-2.

**Ko bangaskiya ya kawasda dokoki goma na Allah?**

"Ta wurin bangaskiya fa muna maida shari'a wofi? Daidai! Ba haka ba; tabbatadda shari'a mu ke yi." Romawa 3:31.

## *Tuba*

**-Wadanne ne anna kiransu zuwa ga tuba?**

"Ni ban zo in kira masu-adilci ba, amma masu-zunubi zuwa tuba." Luka 5:32.

**Nawa ne masu-zunubi?**

"Gama mun rigaya mun kai karar Yahudawa da Helenawa, kalkashin zunubi su ke duka." Romawa 3:9.

**Wadanne irin tambayoyi ne sun fi dacewa da wanda ya zargu ta wurin zunubinsa?**

"Yana'uwa, me za mu yi?" "Ku shugabannai, sai in yi menene domin in tsira?" Ayukan Manzannai 2:37, 16:30.

**Wadanne martani ne maganar Allah ya mayar wa wadannan tambayoyin?**

"Ku tuba a yi ma kowanne daya cikinku baptsma cikin sunan Yesu Kristi zuwa gafarar zunubanku." "sai ka bada gaskiya ga Ubangiji Yesu, za ka tsira ." Ayukan Manzani 2:38, 16:31.

**Menene sakamakon bakinciki ta Allahntaka (ruhaniya)?**

"Gama bacin-zuciya irin da Allah ya ke sa, ya kan aika tuba zuwa ceto." 2 Korintiyawa 7:10

**Menene Yohanna mai-baptisma ya fada wa Farisawa da Sadukiyawa yayinda ya gan zuwa wurin baptismansa?**

"Ku yayan kasaye, way a fadakadda ku ku guje ma fushi mai-zuwa?."Matta 3:7.

## *Furta Zunubai Da Gafara*

**Wane alkawali ne aka yi ma wadanda sun furta zunubansu?**

"Idan mun fadi zunubanmu, shi mai-alkawali ne, mai-adilcikuma, da za shi gafarta mana zunubanmu, shi tsarkake mu daga dukan rashin adilci." 1Yohanna 1:9.

**Wadanne sakamako dabam dabam ne su kan bi rufa zunubai a gefe daya da kuma furta su a daya gefen?**

"Wanda ya rufe laifofinsa ba za ya yi albarka ba; amma dukan wanda ya fade su ya kwa rabu da su za ya sami jinkai."Misalai 28:13.

**Menene Allah yana shirya ya yi ma dukan wadanda sun nemi gafara?**

"Ya Ubangiji, ka kasa kunne ga addu'ata; ka saurara ga muryar roke-rokena."Zabura86:5

**Bisa kan menene Dauda ya kallafa begensa na gafara?**

"Kayi mani jinkai ya Allah, bisa ga rahamarka: bisa ga yawa jiyejiyen kanka ka shafe laifofina." Zabura 51:1.

**Sa'anda Dauda ya furta zunubansa, menene abinda ya ce Allah ya yi?**

"Na dauki zunubina a gabanka; ban boye muguntata ba: na ce na fadi laifofina ga Ubnagiji; kai ma ka gafarta muguntar zunubina." Zabura 32:5.

**Wane galgadi ne ke kallafe bisa ga cewa Allah ya gafarta mana?**

"Ku kasance da nasiha zuwa ga junanku, masu-tubshin zuciya, kuna yi ma junanku gafara, kamar yadda Allah kuma cikin Kristi ya gafarta maku."Afisawa 4:32.

**Ta wurin wanene ake bada tuba da gafara zunubai?**

"Allahna, Ubnagiji Yesu,wanda kuka kashe, rataye shi bisa gungume. Wanda Allah ya daukaka shi da hanun damansa shi zama tsarki da mai-ceto, domin shi bada tuba ga Isra'ila da gafarar zunubi kuma ." Ayukan Manzani 5:30-31.

## *Ruhu Mai-Tsarki Da Aikin Sa*

**Wane alkawali mai kyau ne Yesu yayi ma almajirnasa dab da giciyewansa?**

"Nima in roki Uban, shi kuma za ya baku wani mai-taimako domin shi zamna tare da ku har abada." Yohanna 14:16.

**Don menene Kristi ya tafi?**

"Duk da haka ina fada maku gaskiya; yana da anfani a gareku in tafi: gama idan ban tafi ba, Mai-taimako ba za shi zo wurinku ba; amma idan na tafi zan aiko shi a gareku." Yohanna 16:7.

**Wanene Mai-taimakon, kuma menene aikinsa?**

"Amma Mai-taimako,watau Ruhu Mai-Tsarki, wanda Uban za ya aiko a cikin sunana, za ya koya maku abu, ya tuna maku kuma dukan abin da na fada maku." Yohanna 14:26.

**Menene Karin abinda Mai-taimako zai yi?**

"Shi kwa, sa'anda ya tafo, za ya kada(kalubalance) duniya a kan zunubi, da adilci, da shari'a." Yohanna 16:8

**-Wane suna ne dabam kuma Mai-taimakon ke da shi?**

"Amma sa'anda Mai-taimakon ya zo, wanda zan aiko maku daga wurin Uban, watau Ruhu na gaskiya, wanda ya ke fitowa daga wurin Uba, shi za ya shaida ni." Yohanna 15:26.

**Menene Yesu ya ce Ruhu na gaskiyan zai yi?**

"Amma sa'and shi, Ruhu na gaskiya, ya tafo, za ya bishe ku cikin dukan gaskiya: gama ba za ya fadi daga kansa ba; amma dukan iyakar abinda ya ji, su za ya fadi; za ya bayana maku kuma abin da ke zuwa." Yohanna 16:13.

**Saboda haka, wane kashedi ne aka bayar?**

"Kada kwa ku bata zuciyar Ruhu Mai-tsarki na Allah, wanda aka hatince ku a cikinsa zuwa ranar pansa." Afisawa 4:30.

**Ko akwai kadada game da gaggwarmayar Ruhun Allah?**

"Ubangiji ya ce, Ruhuna ba za ya rika jada mutum har abada ba" Farawa 6:3.

**Domin menene Dauda ya yi addua?**

"Kada ka yashe ni daga gabanka; kada kuma ka dauke mani Ruhunka Mai-Tsarki" Zabura 51:11.

**Wanene ya motsa annabawa domin su bada sakoninsu?**

"Gama ba a taba kawo kowane annabci bisa ga nufin mutun ba; amma mutane suka yi Magana daga wurin Allah, Ruhu mai-tsarki ne yana motsa su. "2 Bitrus1:21.

**Menene yayan Ruhu Mai-Tsarki?**

"Amma diyan Ruhu kamna ne, farinciki, salama, tsawon jimrewa, nasiha, nagarta, aminci, tawali'u, kamewa."Galatiyawa 5:22-23

**Game da wane kan Magana ne ya kamata a sanarda mu?**

"Yanzu, yan'uwa a kan zancen bayebaye masu-ruhaniya ba ni so ku rasa sani." 1Korinthiyawa 12:1.

**Wadanne bayebaye ne an bayar?**

"Kuma Allah ya sanya mutane a cikin ikklesiya, na farko manzanni, na biyu annabawa, na uku masu-koyaswa, kana ayuka, kana bayebaye na warkaswa, taimakai, dabarun mulki, harsuna iri-iri" 1Korinthiyawa 12:28.

## *Baptismar Krista*

**Wane hidima ne an fi danganta shi da gaskanta bisharan?**

"Ya kuma ce masu, ku tafi cikin duniya duka ku yi wa'azin bishara ga dukan hallita. Wanda ya bada gaskiya, kuma a yi masa baptisma, za ya tsira; amma wanda ya ki bada gaskiya za a kashe shi".Markus16:15-16.

**Yaya ne mutane sun ba da hankali ga wa'azin Yohanna mai-baptisma?**

"Sa'annan mutanen Urushalima, da dukan Yahudiya, da dukan wurare na kewaye da Urdun, suna fita zuwa wurinsa; ya yi masu baptisma cikin kogin Urdun, suna fadin zunubansu". Matta 3:5-6.

**Menene manzo Bitrus ya danganta da baptisma a cikin jawabinsa kan rana Pentecost?**

"Bitrus ya ce masu, ku tuba, a yi ma kowane daya cikinku baptisma cikin sunan Yesu Kristi zuwa gafarar zunubanku; za ku karbi Ruhu mai-tsarki kyauta kuma" Ayukan Mazanni 2:38.

**Dangane da baptismar Krista, menene akan wanke?**

"Yanzu fa, don me kake jinkiri? Ka tashi a yi maka baptisma, a wanke zunubanka, kana kira bisa sunansa." Ayukan Manzanni 22:16. Duba Titus 3:5; 1Bitrus 3:21.

**Ta wurin menene a ke wanke zunubai?**

"A gareshi wanda ya ke kamarmu, ya kwance mu daga zunubanmu cikin jininsa." Ruya 1:5.

**Sa'anda an yi ma masu-bada gaskiya ga Kristi baptisma, wanene sukan yafa?**

"Gama iyarka wadanda aka yi maku-baptisma zuwa cikin Kristi kuka yafa Kristi". Galatiyawa 3:27.

**Wane irin dandanon rayuwa ne wadanda aka yi masu baptisma cikin Kristi sukan shiga?**

"Ko kwa kun rasa sani dukanmu da aka yi mana baptisma zuwa cikin Yesu Kristi, zuwa cikin mutuwatasa aka yi mana baptisma?" Romawa 6:3.

**Yaya ne an kwatanta wannan baptisman?**

"Aka bizne mu fa tare da shi ta wurin baptisma zuwa cikin mutuwa: domin kamar yadda aka tada Kristi daga matattu ta wurin darajar Uba, hakanan mu kuma mu yi tafiya cikin sabontakar rai." Aya 4.

**Ta wurin wannan, yaya ne mun sami cikakken hadewa da Kristri a cikin dandanon rayuwa mutunwansa da tashinsa?**

"Gama idan mun hadu da shi bisa ga sifar mutuwatasa, za mu kuma kasance haka bisaga sifar tashinsa."Aya 5.

**Wane tambaya ne mutumin Habashan nan yayi bayan da Filibus ya yi masa wa'azin Yesu Kristi?**

"Ananan suna cikin tafiyarsu, suka zo wurin wani ruwa; baban ya ce ,Ga ruwa; me za ya hana a yi mani baptisma." Ayukan manzanni 8:36.

**Domin ya yi masa baptisma, ina ne Filibus ya kai shi?**

"Ya umurta a tsaida karusa: su biyu fa suka sabko suka shiga ruwa, da Filibus da baban; ya yi masa baptisma." Aya 38.

**A farkon aiki bishara, wane kwatanci ne Yesu ya bari a madadin mabiyansa?**

"Sa'anan Yesu ya tashi daga Galili zuwa Urdun wurin Yohanna, domin shi sami baptisma daga gareshi." Matta 3:13

## *Baiwa Na Bayaswa*

**Menene Kristi ya fada game da albarkun bayaswa?**

"A cikin abu duka na yi maku gurbi, da wahalar kanku hakana ya kamata ku taimaki marasa-karfi, ku tuna da kalmomin Ubangiji Yesu, da ya fadi da kanda, bayaswa ta fi karbawa albarka." Ayukan Manzanni 20:35.

**Wane azumi ne mai-karbuwa ga Ubangiji?**

"Ko ba shi ne azumi da na zaba ba?... ko ba shi ba ne, a rarraba abincinka ga mayunwata, fakirai da an yasda su ka kawo su cikin gidanka? Sa'anda ka ga matsiraici, ka yi masa sutura, ba ka buya ga yan'uwanka ba?" Ishaya 58:6-7.

**Wanne ne wani hanya da aka umurce mu mu girmama Allah?**

"Ka girmama Ubangiji da wadata , da nunan fari na dukan gallarka." Misalai 3:9.

**-Wane bangaren wadatanmu ne Ubangiji ya ce nasan ne?**

"Dukan zakkar kasa kuma, ko na hatsi, ko na yayyan itace, na Ubangiji ne: mai-tsarki ne ga Ubangiji." Leviticus 27:30.

**Domin tallafan wanene, kuma**

**domin wane aiki ne akan kebe zakka a Isra'ila?**

"Ga yayan Levi kuma, duba, na bada dukan zakka cikin Isra'ila gado ne, maimakon hidimansu da su ke yi, watau hidimar tent na taruwa." Lissafi 18:21.

**Wane laifi ne akan sami mutum da aikatawa idan ya ki mayas da zakka bai kuma bada sadaka ba?**

"Mutum za ya yi ma Allah kwace? Duk da haka kwace ku ke yi mani , amma kun ce, a ina fa muka yi maka kwace? A wajen zakka da hadayu (sadakoki)." Malachi 3:8.

**Game da menene Ubangiji ya ce mu gwada shi, kuma bisa ga wadanne sharida ne ya yi mana alkawalin manyan albarku?**

"Ku kawo dukan zakka a cikin ma'aji, domin abinci ya samu a gidanna, ku gwada ni hakanan yanzu, in ji Ubangiji mai-runduna, ko ba zan bude maku sakatan sama ba, in zubo maku da albarku ba; kuringarku kuma ba za ta kakkabe yayanta kamin lokaci ya yi a cikin gona ba, in ji Ubangiji mai-runduna."Malachi 3:10-11.

**Da wane irin ruhu (ko manufa) ne ya kamata mu yi bayaswa?**

"Kowane mutum shi aika bisa yadda ya annita a zuciyassa; ba da cicijewa ba, ba kwa kamar ta dole ba; gama Allah yana son mai-bayaswa da dadin rai." 2 Korintiyawa 9:7.

**Menene Kristi ya fada game da bayaswa?**

"Bayaswa ya fi karba albarka" Ayukan Manzanni 20:35.

**Bisa ga menene bayaswa ya kan sami karbawa?**

" Gama idan nufi(mai kyau) yana nan, abin karba ne gwalgwadon abin da wurin mutum, ba gwalgwadon abin da ba shi da shi." 2 Korintiyawa 8:12.

**Kristi ya aike almajiransa su je su yi wa'azi, su warkasda marasa-lafiya, su kuma tada matattu, menene ya ce masu?**

"Kyauta kuka karba, sai ku bayas kyauta" Matta 10:8

## *Yanayi Mai-Kyauna Na Lafiya*

**Wane fata ne Manzo Yohanna ya yi ma Gayus?**

"Kamnatacena, ina yin addu'a ka sami albarka cikin dukan al'amura, ka kasance da lafiya kuma, kamar yadda ranka yana albarka." 3 Yohanna 2.

**Don menene ya kamata a kiyaye lafiyan jiki?**

" Gama aka saye ku da tamani: ku daukaka Allah fa cikin jikinku.: 1 Korintiyawa 6:20.

**Menene an kira jikin?**

"Ko baku sani ba jikinku, wanda kun karba daga wurin Allah ? Ku kwa ba na kanku ba ne." Aya 19.

**Wane martini (tasiri) ne fara'a ya ke da shi ga lafiya?**

"Zuciya mai dadi magani ce mai-kyau." Misalai 17:22.

**Yaya ne Kristi ya tanada hutu ga almajiransa?**

"Ya ce masu, ku zo da kanku waje daya inda ba kowa, ku huta kadan." Markus 6:31

**Yaya ne aka galgade mu mu mika jikinmu ga Allah?**

"Ina rokonku... ku mika jikinku hadaya mai-rai, mai-tsarki, abin karba ga Allah." Romawa 12:1.

**Wane kudiri mafi-girma ne ya kamata ya mallake rayuwarmu?**

"Ko kuna ci fa ko kuna sha, ko kwa iyakar abin da kuke yi a yi duka domin a girmama Allah."1 Korintiyawa 10:31.

**Wane kashedi ne an bayar ga wadanda suka jawo wadansu zuwa cikin rayuwa na rashin kamewa?**

Kaitonsa, shi wanda ke ba makwabcinsa sha, kana kara naka dafi gareshi, kana kwa sa shi shi yi maye." Habakkuk 2:15.

**Ko masu shan barasa za su shiga mulkin sama?**

"Da masu-fasikanci, da masu-bautan gumaka,… da barayi, da masu-kyashi, da masu-maye, da masu-alfasha, da masu-kwache, ba za su gaje mulkin Allah ba." 1 Korintiyawa 6:9-10.

**Menene wani sakamako mummuna na rashin kamewa?**

"Kada ka kasance kana cikin masu-shayeshaye: ko wurin masu-zarin cin nama: gama mai-maye da mai-zarin ci za su yi talauci." Misalai 23:20-21.

KA LURA: "Taba wata boyayyar guba ce wanda ta fi kowane wannan yanayin bisa ga fahintar masu kimiyyan sinadarai, ban da wannan ruwan batir mai hallakaswa(watau prussic acid)" *M. Orfila, Shugaban Makarantar aikin Likita ta Paris*.

**-Menene abinci na asali da aka tanada?**

"Allah kuma ya ce, ga shi na bada kowane ganye mai-bada kwaya da ke bisa fuskar duniya duka, da kowane itace, wanda diyar itace mai-bada kwaya yana cikinsa; shi zama abincinku." Farawa 1:29.

KA LURA: A wata hausan ana nufin, ganyaye, hatsi, yayan itatuwa da kwayoyi masu mai(kamar su gyada).

**Allah ya zabi Isrra'ila domin su zama mutanensa, wadane irin namomi ne kwa a rubuce daga abincinsu?**

Wadanda an kira su marasa tsarki. Duba Leviticus 11 da Kubawar Shari'a 14.

## *Ina Ne Matattu Suke?*

**Yaya ne Littafi Mai-tsarki ya kwatanta barci?**

"Amma bamu so ku da jahilci, yan'uwa, ga zancen wadanda sun yi barci; kada ku yi bakinciki kamar sauran mutane, wadanda basu da bege." 1 Tassalunikawa 4:13. duba kuma 1 Korintiyawa 15:18,20, Yohanna 11:11-14.

"Dayawa kwa daga cikin wadanda su ke barci cikin turbayar kasa za su falka." Daniel 3:20. 9:10.

**Ko matattu masu-adilci suna sama ne suna yabon Allah?**

" Gama Dauda ba ya hau cikin sammai ba." Ayukan Manzanni 2:34. "Matattu bas u yabon Ubangijiba, babu mai-yabin kuma cikin masu-gangarawa wurin shuru." Z abura 115:17.

**Ko wani ya kan san game da Allah sa'anda ya rigaya ya mutu?**

"Gama cikin mutuwa babu tunawa da kai." Zabura 6:5.

**A yanayin nan na mutuwa, menene mutum ya kan sani game da iyalinsa?**

"Yayansa sun sami girma shi ba ya sani ba; sun sha kankanci, ba yaji komi ba." Ayuba 14:21.

**Me ke faruwa da tunanin mutum a mutuwa?**

"Lumfashinsa ya kan fita, ya kan koma turbayassa kuma; a cikin wannan rana shawarwarinsa su kan lallace." Zabura 146:4.

**Ko matattu sun san wani abu?**

"Gama masu-rai sun san za su mutu amma matattu ba su san komi ba." Mai-wa'azi 9:5.

**Ko su kan shiga cikin harkokin rayuwa?**

"Kamnarsu duk da kiyayyassu, da kishinsu, yanzu sun kare; ba su kwa da wani rabo har abada a cikin komi da a ke yi a cikin duniya" Aya 6.

**Yaushe ne tashin matattu na masu-adilci zai gudana?**

"Gama Ubngiji da kansa za ya sabko daga sama , da kira mai-karfi, da muryar tsarkin mala'iku, da kafon Allah kuma: matattun da ke cikin Kristi za su fara tashi" 1 Tassalunikawa 4:16.

**Menene ya zo kan dukan mutane sakamakon faduwa cikin zunubi?**

"Cikin Adamu duka suna mutuwa" 1 Korintiyawa 15:22. duba Romawa 5:12.

**Yaya yawan ayukan da mu kan yi bayan mun mutu?**

"Dukan abin da hannunka ya iske na yi, ka yi da karfinka, gama babu wani aiki, ko dabara, ko ilimi, ko hikima, cikin kabari inda za ka." Mai-wa'azi 9:10.

**Muryar wanene ke tada matattu?**

"Kada ku yi mamakin wannan; gama sa'a tana zuwa inda dukan wadanda suna cikin kabarbaru za su ji muryatasa, su fito kuma: wadanda sun yi nagarta, su ji zuwa tashi na rai; wadanda sun yi mugunta, zuwa tashi na shari'a." Yohanna 5:28-29

**A wadanne kalmomi ne aka bayanna gagarumar nasara ta karshe bisa mututwa da kabari?**

"Ya mutuwa, ina nasarki? Ya kabari, ina karinki?" 1 Korintiyawa 15:55.

**Bisa ga fasalin jiki, wanene za a sarrafa jikunnan wadanda suka tashi daga matattu(masu-adilci)?**

"Muna sauraron Mai-ceto, Ubangiji Yesu Kristi: wanda za ya sake sifanta jikin nan na kakantarmu domin ya yi kama da jikin darajassa." Kolosiyawa 3:20-21.

## *Kafuwar Assabbat*

**Yaushe ne aka yi Assabbat kuma ta wurin wa?**

"Aka gama aikin sama da kasa, da dukan rundunansu. A kan rana ta bakwai fa Allah ya gama aikinsa wanda ya yi; ya huta fa a kan rana ta bakwai daga dukan aikinsa da ya yi." Farawa 2:1-2.

"Kuma Allah ya albarkaci rana ta bakwai, ya tsarkake ta: domin a cikinta ya huta daga dukan aikinsa wanda Allah ya halitta da wanda ya aika." Aya 3.

**Menene dalilin kiyaye ranar Assabbacin da tsarki?**

"Gama cikin kwana shidda, Ubangiji ya yi sama da kasa, da teku, da abinda ke cikinsu duka, ya huta kuma a kan rana ta bakwai: domin wannan Ubangiji ya albarkaci ranar Assabbat, ya tsarkake ta." Fitowa 20:11.

**KA LURA**: Assabbacin abin tunawa ne na halitta. Allah ya shirya cewa ta wurin kiyaye ta, mutum zai ci gaba yana tunawa da shi kamar Mahaliccin dukan abu mai-gaskiya kuma har abada.

**Wace rana ce ranar Assabbat?**

"Rana ta bakwai Assabbat ne." Fitowa 20:10.

**Ko an shirya cewa Assabbat ta**

**zama ranar sujada na jama'a ne?**

"Kwana shidda za a yi aiki; amma rana ta bakwai Assabbat ne ran hutawa mai-sujada, taruwa mai-tsarki." Leviticus 23:3

**-Akan menene kuma Allah ya ce ya badda Assabbat zuwa ga mutensa ya zama shaida, ko tuni?**

"Na kuma ba su sabbatai nawa, su zama shaida tsakanina da su, domin su sani ni ne Ubanhiji wanda ya tsarkakesu." Ezekiel 20:12.

**Yaya ne yawan tattaruwan fansassu zai kasance domin sujada zuwa ga Ubangiji?**

"Gama, yadda sabobin sammai da sabuwar duniya wadanda zan yi, za su dawama a gabana, in ji Ubangiji, hakanan kuma zuriyarku da sunanku za su dawama. Za ya zama kuma, daga wani sabon wata zuwa wani, daga wata assababat kuma zuwa wata assabat, dukan masu-rai zasu zo su yi sujada a gabana, ni ji Ubangiki." Ishaya 66:22-23.

**Da wane lokaci ne bisa ga Littafi Mai-tsarki Assabbat yakan fara?**

"Akwai maraiche akwai safiya, kuma, kwana daya ke nan.. da sauransu. Farawa 23:32.

DUBA Markus 1:32.

**Ko Kristi sa'anda yana duniya ya kiyaye Assabbat?**

"Ya shiga cikin majami'a bisa ga al'adatasa ran assabbachi, ya tashi tsaye garin ya yi karatu." Luka 4:16.

**Ko da shike shine Ubangiji, mai kafawa da mai kiyaye ranar assabbat, yaya ne an sa masa ido ana bincikensa akan ranan nan?**

"Marubuta da Farisawa suka zuba masa ido, su ga in ko zaya yi warkaswa a kan assabbachi, domin su sami yadda za su tsare shi." Luka 6:7

**Yaya ne Kristi ya tinkari koyaswowin su na karya game da Assabbat?**

"Yesu ya ce masu… ya halatta ran assabbachi a yi nagarta ne ko kuwa a yi barna? A chichi rai ko kwa a hallaka? Aya 9

## *Ranar Ubangiji*

**Akan wane rana ne Yohanna ya ce yana cikin Ruhu?**

"Ina cikin Ruhu a kan ranar Ubangiji," Ruya ta Yohanna 1:10.

**Wace rana ce doka ta kira ranar Ubangiji?**

"Amma rana ta bakwai assabbat ne ga Ubangiji Allahnka" Fitowa 20:10

**Menene Annabi Ishaya mai sadarwan Allah ya kira Assabbat na rana ta bakwai?**

"Mai tsarki na Ubangiji." Ishaya 58:13.

**To akan wane rana ne Yohanna ya kasance a cikin Ruhu?**

Rana ta bakwai, idan yana nufin wata ranar mako.

**KA LURA**: Ba wata rana a cikin mako da Allah ya kirata ranarSa banda na bakwai din.

**Ko Kristi ya kiyaye Assabbat?**

"Ya shiga chikin majami'a bisa ga ala'adatasa, ran assabbachi ya tashi tsaye garin yayi karatu." Luka 4:16, "Na kiyaye dokokin Ubana." Yohanna 15:10.

**Ko masubin Kristi sun kiyaye Assabbat bayan mutuwarsa?**

"Suka komo, suka shirya kayan kamshi da man kamshi. Suka huta ran assabbachi bisa ga doka."Luka 23:56., "Domin dukan mutane su bada girma ga Dan, kamar yadda su ke bada girma ga Uban." Yohanna 5:23.

**KA LURA**: Mutum a nan yana nufin yan Adam.

**Na menene Kristi ya ce Dan mutum Ubangiji ne?**

"Gama Dan mutum ubangijin assabbachi ne " Matta 12:8. Duba Markus 2:28.

**Wanene ya yi assabbat?**

"Ta wurinsa aka yi dukan abu(watau Kristi, Kalman)" Yohanna 1:3

**Wace rana ce rana ta fari ga mako yake bi?**

"Ananan a karewar ran assabbachi, sa'anda rana ta fari ga bakwai ta kusa wayewa." Matta 28:1

**KA KURA**:Bisa ga sabon Alkawari, wannan ya nufi Assabbat ya shige kennan,s'annan rana ta fari mako (bakwai) ya fara.

**Wace rana ta mako (bakwai) ne Assabbat "bisa ga doka"?**

"Amma rana ta bakwai Assabbat ne ga Ubangiji Allahnka" Fitowa 20:10.

**KA LURA:** Akwai tabachin cewa assabbat na sabon alkawali daya ne da assabbat na tsohon alkawali, da kuma cewa babu wani abu a sabon alkawali day a kawas da assabbat na ran ta bakwai, ya kuma mayas da rana ta fari ga mako a madadin shi.

**Ta wurin banbantuwa da masu sujada ga bisan, yaya ne an bayana masu sujada ga Allah?**

"Na ga hankurin tsarkaka, su wadanda ke kiyaye dokokin Allah, da imanin Yesu." Ruya ta Yohanna 14:12.

## *Sake (Canjin) Assabbachi*

**Yaya ne kiyaye Lahadi ya fara?**

Yawanci sun gaskanta da cewa Kristi ya sake assabbat, amma, daga kalmomin bakinsa, mun ga cewa ba ya zo da wani shiri kamar haka ba. Alhakin wannan canjin dole a dube shi daga wani wuri da bam.

**A cikin sanannen wa'azinsa, menene Kristi ya ce game da dokan?**

"Kada ku zache na zo domin in warware Attaurat da Annabawa: ban zo domin in warware ba, amma dominin chichika." Matta 5:17.

"Har sama da duniya su shude, ko wasali daya, ko digo daya ba za ya shude daga Attauratba, sai dukan abu ya chika." Aya 18.

**Menene Allah, ta wurinAnnabin Daniyel(Daniel) ya ce ikon da kankanin kahon nan ya misalta zai yi tunanin aikatawa?**

"Zaya yi maganan ruba sabanin Madaukaki, za ya kwa gajiyadda tsarkaka na Madaukaki: za ya nufa ya sake zamanu da shari'a kuma." Daniel 7:25.

**Wace mulki ce ta yi korafin iko na sake Dokan Allah?**

"Mulki Paparoma.

**KA LURA**:Paparoma yana da babban izini da iko da zai iya daidaita, ya bayana, ko kuma fasara, har ma da dokokin Allah…. Paparoma zai iya daidaita dokan Allah tunda ikonsa bana mutum ba ne, amma na Allah , kuma yana tsaye a madadin Allah ne a bisan duniya" fara da *Lucius Ferraris, Prompta Bibliotheca(Ready Lebarary), "Papa", art, 2.*

**Doka ta hudu**

**"**Ita (Ikklesiyar Katolika) ta sake doka ta hudu ta wurin kawasda Assabbat na Kalmar Allah, kuma ta kafa Lahadi a masayin rana hutu" *N. Summarbell, History of Christian Church (1873) p, 415.*

"Lahadi, kamar rana na mako da aka kebe a masayin doka domin sujadan dukan jama'a zuwa ga Allah, don tsarkakewa ta wurin janyewa daga aiki mai zafi; kasuwanci da dukan hidima na duniya, da kuma mika kai, babu shakka halita ne na Ikklesiyar Katolica." *The Amerian Catholic Quaterly Review, January, 1883, PP, 152, 139.*

"Idan Ikklesiyar da suka ki ikon Katolika, za su bi Littafi Mai-Tsarki, za su yi sujada ga Allah akan ranar Assabbat ne. Ta wurin kiyaye Lahadi suna bin doka ne na Ikklesiyar Katolika. *Albert Smith, Chan Cellor of the Archdiocese of Baltimore replying for the cardinal in a letter of Feb. 10, 1920.*

**Wadane koyaswa ne mutane suka sake (musaye) da Kalmomin Ruhu da gaskiya?**

"Amma a banza suke yi mani sujada, koyaswa da su ke yi dokokin mutane ne…. ya chemasu, sarai ne kuna kin dokar Allah domin ku kiyaye takalidinku." Markus 7:7-9.

"Har yaushe za ku yi dingishi a kan wannan imani da wanchan? Idan Ubangiji shi ne Allah, bi shi; amma idan Baal ne sai kubi shi." Sarakuna ta 1,18:21.

## *SAKON ALLAH NA KARSHE ZUWA GA DUNIYA NA ZUNUBI*

Yesu ya ce, "wannan bishara kwa ta mulki : za a yi wa'azinta chikin iyakar duniya domin shaida ga dukan al'umai; sa'annan matuka za ta zo." Matta 24:14.

Mai karatu chikin wannana karamar mujalan za ka sami cikakken bayani game da bisharan Yesu Kristi, kamar yadda aka bayar a cikin Littafi Mai-tsarki, ba tare da takaludai da koyaswar mutane ba.

"Da babbar murya kwa ya ce, ku ji tsoron Allah, ku bashi daraja; gama sa'ar hukunchinsa ta zo." Ruya ta Yohanna 14:7.

Hukuncin (shari'an) Allah ta fara ne a cikin sama a shekara ta 1844. Ta fara ne da matattu. Matattu ba su sama, suna kwance a cikin kabari, suna jiran tashin matattu." Wadansu zuwa raina har abada, wadansu kuma zuwa kumya da reni mara-matuka." Daniel 12:2.

Ba da jimawa ba, ba wanda ya sani ko yaushe, hukunchin (shariyan) zata fara akan masu rai.

"Ku yi sujada ga wanda yayi sama da duniya da teku dama bulbulan ruwaye."

Babu mutum, ko Paparoma, ko firist, ko mai wa'azi wanda zai iya gafaran zunubi. Ba mutumin da ya cacanci karbar sujada. "Yesu ya ce masa, rabu da nan, ya Shaitan. Gama an rubuta, ka yi sujada ga Ubangiji Allahnka, shi kadai ma zaka bauta masa." Matta 4:10.

Maryamu maman Yesu tana cikin kabarin ta ba zata iya taimakon ko

mutum daya ba.

Yesu ya ce, "Da ni da Ubana daya ne. Yuhudawa suke daukan duwatsu da za su jejjefe shi. Yesu ya amsa masu ya che, kyawawan ayuka da yawa na nuna maku daga wurin Uban. Sabo da wane aiki a chikinsu kuna jejjefata? Yahudawa suka amsa suka ce, sabo da kyawawaan aiki bamu jejjefe ka ba, amma domin sabon Allah, kuma domin kai da kake mutum, kana maida kan ka Allah." Yohanna 10:30-33.

"Na san….zagin (sabo) na wadannan da ke che da kansu Yahudawa(mutanen Allah na gaskiya) ba kwa haka suke ba, amma majami'ar shaitan ne." Ruya ta Yohanna 2:9.

"Ya kuma che mani….lokachi ya kusa (ko yayi). Wadanda shi ke ma-adilci, bari shi yi ta rashin adilci:wanda shi ke mai-kazamta kuma, a kara kazamtadda shi:….gashi, ina zuwa da samri; hakina yana tare da ni kuma, saka ma kowane mutum gwalgwadon aikinsa…

Daga waje da karnuka, da masu-sihiri, da fasikai, da masu-kisankai, da masu-bautan gumaka, da dukan wanda yana kamnar karya yana kwa aikatata." Ruya ta Yohanna 22:10-12, 15.

" Sai wani, kuma mala'ika na biyu ya bi bayansa, yan chewa, Ta fadi, Babila babba ta fadi." Ruya ta Yohanna 14:8.

## *Wanene Babilan?*

Littafi Ruya ya dauki sunaye da wurare da kuma al'amura daga babban da suka fara a sarari, a cikin tsohon alkawali ya kuma yi anfani da wadannan sunaye da alamura a hanya na sabon alkawali.

A cikin Ruya, Babila an yi anfani da ita ne don bayana fadaddun Ikklesiyoyi:

Domin "ta sa dukan al'umai sun sha ruwan anab na hasalar faskanchin ta."Ruya 14:8.

Belshazzar ya kaskantar da Allah ta wurin anishuwar buguwar giya:

"Suka sha ruwan anab, suka yi yabon alloli na zinariya da na azzurfa, na jangachi, na bakin karfe, na itace da na dutse." Daniel 5:4.

"Da Babila kokon zinariya ne a cikin hanun Ubangiji; koko wanda ya sa dukan duniya ta yi maye; al'ummai suka sha ruwan anab na ta; sun yi hauka fa."Irmiya 51:7.

Babila misali ne na **ADININ** kariya kuma **RUWAN ANAB MISALI NE NA KOYASWOYINTA.**

"Sai daya cikin mala'kun nan bakwai wadanda ke da bakwai din kasake (kaskoni) ya zo, ya yi zanche da ni, ya che, ka zo daga nan, in nuna maka hukunchin (Ruwaye masu-yawan yana misalta mutane da taron jama'a da al'ummai da harsuna Ruya 17:15.) wanda sarakunan duniya suka yi fasikanchi da ita, mazamnan duniya kuma suka yi maye da ruwan anab na fasikanchita…Machen kuma tana yafe da shunaiya da mulufi, tana ado da zinariya da duwatsu masu-tamani da lu'u-lu'ai, chikin hannunta tana da koko na zinariya chike da kazamche-kazamche, watau abubuwa masu-dauda na fasikanchinta; bisa goshinta kuma da suna a rubuche, Asiri, ***BABILA BABBA UWAR KARUWAI DA ABUBUWA MASU-BAN KYAMA NA DUNIYA***. Na ga machen kuma tana maye da jinni tsarkaka da jinin shaidu na Yesu." Ruya 17:1-6.

***MACE*** a cikin anabci yana misalta Ikklesiya, mai kyau, da mara kyau.

Mace mai mugunta (Ikklesiya na karya) ana kiranta karuwa (mazinachiya). duba Ruya 17:1.

Mace mai kyau din (Ikklesiya na gaskiya) ana kiranta budurwa. Duba Ruya 14:4.

Mace mai mugunta tana fasikanchi da sarskuna duniya. Duba Ruya 17:2.

Mace mai kyau din ta yi aure da Kristi. Korintiyawa ta 2, 11:2.

Mace mai muguntan ta yafa shunaiya da mulufi, ta kuma yi ado da zinaruya da dutatsu tamani. Duba Ruya 17:4.

Mace mai kyau din ta yi sutura da linen mai tabshi, tsatsabta kuma fari fat. Duba Ruya 19:8.

Mace mai mugunta tana koyas da takalidai (al'adu) abubuwa masu dauda na fasikancinta. Duba Ruya 17:4.

Mace mai kyau din tana koyas da kalmar Allah Mai-tsarki. Duba Ruya 14:5.

Mace mai muguntan ta kan sa a tilasta ma duniya ta wurin doka su yi biyaya da dokokin adini da mutane suka kirkiro. Duba Ruya 13:15.

Mace mai kyau din tana kiyaye dokokin Allah. Duba Ruya 14:12.

Mace mai muguntan Allah zaya hallaka ta. Duba Ruya 19:20.

Mace mai kyau din zata tsaya da Allah bisa teku na madubi. Duba Ruya 15:2.

"Na ga wani mala'ka yana sabkowa daga sama, yana da hukunchi da yawa; duniya kuma ta haskaka domin daukakassa. Ya tadda murya da karfi ya che, fadadiya che, fadadiya che Babila babba, ta zama gidan aljanu da madamar kowane kazamin ruhu da kowane kazamin tsuntsumai ban kyama. Gama da ruwan anab na hasalar fasikanchinta dukan al'ummai sun fadi; sarakunan duniya kuma suka yi fasikanci tare da ita, dillalan duniya kuma suka wadata bisa ga ikon annishuwanta. Na ji wata murya daga sama ta che, ku fito daga chikinta, ya al'ummata, domin kada ku yi tarayya da zunubanta, kada ku sha rabon alobanta." Ruya 18:1-4. Fitowa daga chikin Babila yana nufin fitowa daga cikin Ikklesiyoyi na karya (rashin gaskiya).

"Sai wani mala'ika kuma na uku, ya bi bayansu, da murya mai-karfi ya che, idan kowane mutum ya yi sujada ga bisan." Ruya 14:9.

## *Wanene Bisan?*

Annabi Daniyelu da ya ga ruyai da mafalkai, ya kuma ga "manyan bisashe guda fudu kumasuka taso daga chikin teku, kamassa dabam-dabam."

"Na farin yana da kamar zaki." Daniel 7:3-4.

***BABILA,*** ta yi mulkin duniya daga shekara ta 606 zuwa 539 BC (kafin Kristi).

"Ga kwa wani bisan, na biyu, mai-kama da byer(bear). Sashinsa daya yah au bisa kan daya." Daniel 7:5.

Bagare daya ya fi dayan karfi. ***MEDES DA PERSIA (PASHIYA***) sun yi mulkin duniya daga shekara ta 539 zuwa 331 BC (kafin Kristi). Mulkin Persia(Pashiya) ta fi karfi kuma itace ta zo daga baya.

"Sai ga wani mai kama da damisa." Daniel 7:6. ***GIRKA*** ta yi mulkin duniya daga shekara ta 331 zuwa 168 BC(kafin Kristi).

"Ga shi wani bisan na fudu, mai-ban razana; mai-iko, mai-karfi, kwarai; ya parpashe, ya tattake sauran da sawunsa; yana kwa da bam da sauran bisashen da suka rigaye shi; yana da kafo kuma." Daniel 7:7. Rom (Roma) ta yi mulkin duniya daga shekara ta 168 zuwa 538. AD (Bayan Kristi).

"hakanan ya che, Bisan nan na fudu za ya kasanche mulki na fudu a bisan duniya." Daniel 7:2-3.

Mulkin (Daular) Rom (Roma) ta rarrabu zuwa mulkoki goma (10) tsakanin 351 da 476 AD.

"Na lura da kafofin, sai kuma, ga wani kofa daga chikinsu ya taso, kankane, ne a gabansa kwa, aka tumbuke guda uku daga chikin kafonin nan na fari: gashi kwa cikin wannan kaho akwai idanu masu-kama da na mutum, baki kuma mai-furtadda manyan ruba." Daniel 7:8.

Wannan kankanin kafon shi ne bisan Ruya 14:9, MULKIN PAPAROMA

Kafin Ikklesiyar Paparoma ta samu cikakken mallaka na gwamnati, sai da ta kawas da uku daga chikin kafoni goma din nan, *Heruli,Vandals da kumaOstrogoths.* Wadannan mulkoki na Ariyawa (arians) an maimaye su ne a shekara ta 538 AD (Bayan Kristi) kuma daga wannan shekaran mulkin Paparoam ta fara mulki ta bisa sarakuna na duniya na tsawon shekaru 1260. AD 538 zuwa 1798 – ka duba Tsarin bayani.

"Ina ta dubawa, sai wannan kafo ya yi yaki da tsarkaka har ya rinjaye su; …za ya yi maganar ruba sabanin Madaukaki, zaya kwa gajiyadda tsarkaka na Madaukakai; za ya nufa ya sake zamanu da shari'a (Dokoki) kuma:za a bashesu chikin hannunsa har wokachi daya da wokatai da rabin wokachi." Daniel 7:21-25.

"Zasu tattake birni Mai-tsarki (Ikklesiyar Allah na gaskiya) kalkashin sawaye wata arba'in da biyu." Ruya 11:2

"Machen (Ikklesiyar Allah na gaskiya) kuwa ta gudu zuwa chikin jeji, inda Allah ya rigaya ya shirya mata wurin da zata yi mata kiwo a chan kwana dubu da metin da sittin(1260)." Ruya 12:6.

Ikklesiyar Rom ta Katolika ta sannanta ma Ikklesiyar Allah na gaskiya na tsawon shekaru 1260, AD 538 zuwa 1798.

## *Kisan Milyoyin Jama'a Domin Gaskiya*

"Batun cewa Ikklesiyar Rom ta zubar da jinin marasa laifi fiye da kowane kungiya da ta taba rayuwa a chikin yan adam ba wani daga Ikklesiyoyin da suka ki ikon Katolika (protestant), wanda ke da cikakken sani na tarihi wanda zai musanci wannan. Yana da wuya a samu cikakken fahimi game da yawan jama'a da suka hallaka, kuma akwai tabacin cewa babu wani iko na tunani da ya isa ya kiyasta wahalan da suka. *W.E.H.Leeky History of the spirit of Rationalism in Europe. Vol 2:32, 1910 edition.*

Bayani mai kyau sosai, ko da shike mai-tsawo, da ke bayana wa kud-da-kud dama(yanchi) na Ikklesiyar Rom na Katolika na yin wannan ana samunsa a chikin *Catholic Encyclopedia, vol. 12:266.*

"Don riken bangaskiya da ban da koyaswowin Ikklesiyar Rom, tarihi ta lisafta kisan masubi fiye da miliyon dari

**Wadannan nasosin Littafi Mai-Tsarki sun bamu ginshikin lisafi na lokaci na anabci-kwana daya daidai yake da shekara daya:**

**"Gwalgwadon kwanakin da kuke gewayar kasa, kwana arba'in ke nan, shekara arba'in guda mamakon kowache rana." Littafin Lissafi 14:34.**

**"Na sanya maka rana guda domin shekara guda" Ezekiel 4:6.**

**"Za a bashesu chikin hannunsa har wokachi daya da wokatai da rabin wokachi."**

**Daniel 7:25**

**"Wokachi daya, da wokatai, da rabin wokachi." Ruya 12:14.**

**Wokachi= shekara daya (1)**

**Wokatai= shekaru biyu (2)**

**Rabin wokachi= rabin shekara(1/2)**

**Ta wurin anfani da kirge (lisafi) na anabci, shekara daya (1) ko wokachi= kwana 360.**

**Uku (3) da rabi (1/2) = uku (3)da rabi(1/2) sau (x) 360= kwanaki 1260.**

**Kwana daya (1) = shekara daya(1); kwanaki 1260 = shekaru 1260.**

(100,000,000). Waldenses da Albigenses (ikklesiyoyin da suka ki ikon Katolika na Swiss da Faransa) miliyom daya sun hallaka lokachin yakin fadada adini wanda ***paparoma Innocent na Uku*** ya shelata a shekara ta 1208 AD. Daga lokacin da aka kafa kungiyar mayakar asiri(Jesuits) na Katolika a shekara ta 1540 zuwa 1580, dubai dari tara ne (900,000) aka hallaka . mutum dubu dari daya ne da hamsin(150,000) suka hallaka ta wurin Kotun tuhuma a shekaru talatin. A cikin tsawon shekaru talatin da takwas bayan umurnin ***Charles na biyar***, sabanin Ikklesiyoyin da suka ki ikon Katolika, mutum dubu hamsin (50,000) ne aka kashe ta wurin ratayawa ko yanka kai ko Konawa da rai a masayin masu koyaswan karya. Wadansu dubu-

"Goma sha takwas (18,000) sun hallaka a lokachin mulkin ***Basarake Alvan*** a tsawon shekaru biyar da rabi." *Brief Bible Reading. P. 16*

John (Yohanna )***Wycliffe*** jarumin mutum Allah, ya sha raini ko (kaskanci) a hannun yan paparoma sosai yanda har bayan shekaru arba'in (40) da mutuwansa, an hake kasusuwansa an kone su a gaban taron kama'a. ta wurin rubuce-rubucensu ne yawancin kura-kurai na adinin Romawa ya bayanu.

Huss da Jerome dukansu an kone su zuwa ga mutuwa bayan an daure su akan itace. Sun ki su janye daga wa'azin gaskiya, domin haka shugabanin Katolika suka bada su zuwa ga harshen wuta. (duba Wylie,b3, ch 17).

Game da paparoma, ***Martin Luther (LUDA)*** ya rubuta "abun ban tsoro ne ka dubi mutum wanda ya iza ma kansa masayi na wakilin Yesu Kristi yana nuna daukaka da wani Basarake da ya taba yi. Ko wannan itace hanya na kasancewa kamar Patararren Yesu, ko kuma Bitrus mai kaskanci? Shine suka ce, Ubangijin wannan duniya! Amma Kristi wanda shi yake fahariya wakilinsa ne, ya ce, mulkina ba na wannan duniya bane.' (Yohanna 18:36). Ko ma haka mulki na wakilin Kristi ya kamata ya fi na shugabansa?"

Luther ya ce : na raina na kuma kalubulace ta, [umurni na paparoma (a rubuce) wanda ya tabbatar da hukuncin Luther] a matsayin mara mika kai mai karya…. Na yi murna don kasance wa a cikin wannan mummunan yanayin akan adilai mafiya kyau. A yanzu ma na samu yanci mai girma a chikin zuciya ta ; don a karshe na sani da cewa Paparoma shine magabcin Kristi, kuma kursiyin (kujeran) sa na shaitan ne da kansa."*D'Aubigne, B.6, Ch9*

## Yunkuri Na Sake Assabbachi

Mulkin paparoma za "za ya nufa ya sake zamanu da shari'a (dokoki) kuma ." Daniel 7:25.

"Paparoma yana da babban izini da iko da iya daidaita, ya bayana, ko kuma fasara har ma dokokin Allah…. Paparoma zai iya daidaita dokan Allah tunda ikonsa bana mutum ba ne, amma na Allah, kuma yana saye a madadin Allah ne a bisa duniya." Fasara daga *Lucius Ferraris Prompta Bibliotheca, Popa. Arta 2*

*"*Babu shakka Ikkklesiyar Katolika ta yi korafin cewa sake (Assabbachi zuwa Lahadi)a jikinta ne. Da ban zata iya yin mafalki na yin wani abu a zancen ruhaniya ko Ikklesiya da adini ba, idan ba haka ba, kuma wannan **AIKIN SHAIDAN** ikonta ne a zancen adini." *James Cardinal Gibbons in a letter to J.F Snyder of Bloomington, 11. N0v. 11, 1895.*

**TAMBAYA**"Ko kana da wata hanya na tabatar da cewa Ikklesiyar tana da iko na kafa bukukuwa (idodi) na sharadi?"

**AMSA** – "Da bata da iko irin wannan iko, da bata yi abinda masu adini na zamani sun amince da ita ba, da bata kafa kiyaye Lahadi, rana na fari ga mako (bakwai) ba, sauyi (canji)wanda bata da wani izini daga Littafi Mai-Tsarki."

Babu mutum da zai iya sake dokar Allah Mai-Tsarki; sai dai ya nufa kadai cewa zai iya.

Yesu ya ce, "kada ku zache na zo domin in warware Attaurat da Annabawa: ban zo domin in warware ba, amma domin in chichika."

"Gaskiya fa ni ke fada maku, har sama da duniya su shude, ko wasali daya , ko digo daya ba za ya shude daga Attaurat ba, sai daidukan abu ya chika." Matta 5:17-18.

Bulus ya rubuta "kada ku bari kowane mutum shi rude ku da ko kaka: gama wannan sai riddan ta fara zuwa, mutummen zunubi kuma ya bayanu,, dan hallaka, shi wanda yana tsayaya yana kwa daukaka kansa gaba da dukan abinda ake che da shi Allah, ko abinda ake yi masa sujada; har yana zamne cikin haikalin Allah, yana shelar kansa shi Allah ne."Tassalonikawa ta 2, 2:3-4.

"Paparoma shine babban mai martaba kuma mai daukaka yanda shi ba Kaman mutum ne kadai ba, amma kamar Allah, kuma a madadin Allah. Paparoma ta dalilin martaban daukakarsa mai girma ana kiransa **Limamin (bishop**)na limaman Krista. Shi daya ne sarkin na Allahntaka da kuma Basarake mafiya girma, da kuma sarkin sarakuna. Domin haka, an nada ma Paparoman da kambi mai hawa uku, don masayin sarkin sama da na duniya da na kalkashin duniya." *Lucius Ferraris, Prompta Bibliotixeca, vol. 6, P29.*

"Ka tabatar mani daga Littafi Mai-Tsarki kadai cewa dokace in kiyaya Lahadi da tsarki. Babu irin wannan doka a Litafi Mai-Tsarki! Dokace na Ikklesiyar Rom mai tsarki kadai. Littafi Mai-Tsarki y ace, "ka tuna da ranar assabbchi domin a kiyayeta da tsarki." ;Iklesiyar Katolika ta ce, "**BABU**! Ta wurin ikon allahntaka na kawas da ranar assabbat na dokace ku; ku kiyaye rana ta fari ga mako da tsarki. Kuma ku duba ! gaba dayan duniya da wayewanta ta bada kai garin biyaya ta ban girma ga dokan Ikklesiyar Katolica mai tsarki"*Priest Thomas Enrihgt,C.S.SR., President of RedemptionsCollege, Kansas city, Mo. In a lecture at Hartfold, Kansas fe.18, 1884and in the American Sentinel, a Roman catholic journal of june 1883, 173.*

"Na ga wani bisa kuma yana fitowa daga chikin kasa; yana da kafo biyu kamar dan rago, yana kwa zanche kamar dragon.

"Dakan hukumchin bisan na fari kwa yana aiki da shi a gaban idonsa. Yana sa duniya da mazamnan a chikin su yi sujada ga bisa na fari, wanda bugunsa na ajali ya warke." Ruya 13:11-12.

## Shaidar Bisan

"Idan kowane matum ya yi sujada ga bisan da gumkinsa, ya karbi shaida kuma a goshinsa ko a hannunsa,"Shi kuma za ya sha ruwan anab na hasalar Allah, wanda an shirya chikin koko na fushinsa, ba a kwa surka shi ba; za ya sha azaba kuma da wuta da kibiritu a gaban idanun malaiku masu-tsarki, a yaban dan rago kuma:" Ruya 14:9-10.

## Shaida Bisan Iitace Sujada Ranar Lahadi

"Idan kowane mutum ya yi sujada ga bisan da gumakansa, ya karbi shaida kuma a goshinsa ko a hannunsa, "shi kuma za ya sha ruwan anab na hasalar Allah, wanda an shirya cikin koko na fushinsa, ba a kwa surfa shi ba,; za ta sha azaba kuma da wuta da kibiritu a gaban idanun mala'iku masu-tsarki, a gaban Dan-rago kuma:"

wanda za'a tilasta tawurin doka (umurni)-Wannan **SHAIDACE** ta ikklisiyar Rom ta katolika.

Ikklisiyar katolika ta ce , "Babu shakka ikklisiyar katolika tayi korafin cewa sakewar(Assabbat zuwa Lahadi) aikinta ne… kuma aikin S**HAIDA** ne na ikkonta a zancen adini" *Cardinal Gibbons, Nov 11, 1895.*

Kasar Amirka bada jimawa ba zata mayar da iko na kasa (gwamnati) a hannun mulkin paparoma.

"Yana rudin mazamnan duniya kuma saboda alamun da aka bashi shi aikata a gaban idon bisan; yana che ma wadanda ke zamne a duniya, su yi gumki ga bisan wanda ya sha bugun takobi ya kwa yi rai."

"Aka ba shi, ko kuma da za ya bada lumfashi gareshi watau ga gumki bisan, domin gumkinsa bisan shi yi Magana har kuma shi sa a kashe iyakar wadanda ba su yi sujada ga gumkin bisan ba."

"Kuma yana sa a ba dukan mutane, kanana da manya ma wadata da matalauta, yaya da bayi, shaida chikin hannunsa na dama ko a bisa goshinsu;"

"Na ga dayan kawunansa sai ka che an yi masa bugun ajali." Ruya 13:3

"Idan an kadara kowane mutum (ko, shi wanda yake kaiwa bauta) ga bauta, gabauta za shi idan kowane mutum za ya yi kisa da takobi, da takobi za a kashe

shi." Ruya 13:10.

Mun rigaya mun nuna cewa mulkin paparoma za ta yi mulki duniya fiye da tsawon shekaru 1260-AD 538. zuwa 1798 Duba Tsarin bayani.

A shekarata 1798 mulki na wahala ta ci gaba ta wurin babban tawaye na Faransa, sa'annan an kawas da adinin Katolika gafe sojojin Faransa, a kalkashin jagorancin janar **Batiya** (**Berthier**), sun shigo Rom suka damke paparoma zuwa gida yari (firsina). Kwanan watan itace; ***Febrairu, 10,1798***.Daurarren Paparoman ya mutu a gidan bauta a shekara na biya a garin ***Valens(Valence***) na Faransa. An ji kuka mai girma tana cewa "adinin katolika ta mutu." Mulkin paparoma ta sami "bugun ajali". Duba Ruya 13:3. Amma an fada mana cewa bugun ajali ya warke, kuma lokaci yana zuwa ba da jimawaba da dukan duniya za su yi "mamaki da bisan".Duba Ruya 13:3

A shekara ta ***1929 kadinal Gasparre*** ya sadu da shugaba ***Mussolini*** a cikin fadan tsarkaka ***Yahaya (John)Lateran*** inda suka sa hannu a yarjejeniyan ***vatikan***, na mayar da iko na duniya zuwa ga mulkin paparoma; aka kuma sake mayar da ita mulki da nata mallakan. (yankin mulki). Amma bugun ajalin bata warke gaba daya ba.

Amma bugun ajalin ba ta warke gaba daya ba.

Bugun ajalin itace rabewar Ikklisiyar Rom daga malakar kasa (gwamnati) kuma sa'anda wannan bugun ajalin zata gama warkewa, Ikklisiyar Rom ta Katolika zata mallaka dokan kasa (gwamnati) kasar Amirka itace sanadiyan wannan. Dukan duniya zata rude (rudu). Za a yi guguwa, da girgizan kasa, da yinwa, da aloba da kuma cucutuka da yawa. Sa'anan da lokaci ta zo ga karshe wadanan al'amuran zasu dada yin muni, kuma ta dalilin haka za a zargi jama'ar Allah da alhakin wannan. Su masu sihiri (ruhohi) da yawanci masu wa'azi za su ce wadannan munanan-abubuwa a halita ba za su fasa faruwa ba sai duka sun girmama tsarkin ranan Lahadi.

**Hanya mafi kyau na girmama Paparoma, Yahaya, Bulus na 2(John Paul II) a cikin gaskiya, daya daga cikin manyan mutane, itace ka dauki koyaswansa da muhimminci; ka saurari kalmominsa ka kuma sa kalmominsa a cikin ayuka anan Amirka. Wannan itace kalubala da dole mukarba. Shugaba George W.Bush; march(maris)21, 2001.**

**Game da kafawar fili na wasanin al'adu na paparoma wanda aka gina a Washington DC kwana nan, Paparoma ya ce, "zamu zo mu dubi wannan a matsayin wata yar karamar Vatican na mu a cikin Amirka." Kamar yadda aka bada rufotu ta wurin Paul Shephard AP mai rubutawa. The Daily News, March (maris) 24,2001.**

Jama'a zasu bidi dokokin tilasta Lahadi. Kasar Amirka zata jagoranci wannan, kuma dukan duniya zata bi bayanta. "Dukan duniya fa ta na mamaki da bisan" Ruya 13:3

"Yana rudin mazamnan duniya kuma saboda alamun da aka ba shi aiki a gaban idon bisan wandada ke zamne a duniya, su yi gumki ga bisan wanda ya sha bugun takobi ya kwa yi rai." Ruya 13:14.

"Na ga kuma kazaman ruhohi uku, sai ka che kwadi, suna fitowa daga bakin dragon, daga bisan kuma, daga bakin mai-karyan anabci kuma: kada kowane mutum kuma shi sami iko shi sayi ko sayas, sai wanda yana da shaidan, watau sunan bisan ko ***number*** na sunansa."

"Na ga hikima wanda ya ke da fahimi, bari shi lissafta nomba na bisan, gama nomba na mutum ne :nombansa kenan***, Dari shidda ne da sittin da shidda(666)."*** Ruya 13:14-18.

Kasar Amirka ta taso ne a cikin shuru daga doron kasa a sakanin shekara ta 1798, kusan lokaci daya da salwancewar(rasa) mulkin Paparoma. Wannan babban al'umman Amirka tana da kaho biyu kamar ta dan rago-al'ummace marasa tsarki kuma ikklesiyay ce marasa paparoma. Al'ummace wanda ta yi fahariyan yanci na adini da kuma democradiya inda kowane mutum dan kasa yana da murya a al'umura na kasan. Amma kaito, wannan babban al'umma ba da jimawa ba za ta yi Magana kamar dragon."

Tsarin mulkin kasar Amirka ta ce "majalisun dokoki ba za a kafa wata doka wanda zai goyi bayan kafa wata adini ko kuma ya hana yin ta ba; kuma ba zata hana yanci na Magana, ko na rubutu, ko daman a mutane su taru a cikin salama su roki Gwamnati ta daidaita (gyara) wani damuwa ba."

***Abraham Lincoln*** a zancensa na ***Gettisboy (Gettysburg)*** ya ce "*Gwamnati na jama'a, ta wurin jama'a kuma domin jama'a."*

Jama'ar kasar Amirka sun kirkiro tsarin mulki wanda ya tanada yanci na adini ga duka. Jama'an kasar Amirka ba da jimawa ba za su, sake, kuma ta wurin zabe, za su bukaci Majalisun dokoki ta sake tsarin mulkinsu. Littafi Mai-Tsarki ya fada mana cewa ta wurin koyaswan ruhohi wani bisan kuma yana fitowa daga chikin teku, mai-kaho goma da kai bakwai….bisa kawunansa kuma sunaye na sabo."

"Bisan (Rom ta Paparoma) da na kuma yana kama da damisa, sawayensa kuma suna kama da na ***byer (bear),*** bakinsa kwa kamar bakin zaki: dragon ***(Rom ta Arna)*** kuma ya ba shi ***(Rom ta paparoma)*** ikonsa da kursiyinsa da hukunchi mai girma…… Dukan duniya fa ta yi mamaki da bisan" Ruya 13:1-3.

Cire karagar (babban Birni) na mulkin daga ***Rom*** zuwa ***Konstan tinopul*** a shekara ta 330 ya bada dama ga ikklisiyar da ke yammaci ta kasance da yanci daga mallaka na sarauta, ta kirkiro nata tsarin, shi Limamin Krista na Rom, wanda ya kasance a kujera na yamancin, kuma ba da jimawa ba an tilasta shi ya zama shugaba na gwamnati (siyasa) da ruhaniya***.*** *A.C. Flick,The Rise of Medieval Church, P. 168*

"Dukan wani asali (al'adu) na Romawa da baibayai (jahilai) da kuma Ariyawa suka bari….a kalkashin tsaro na Limamin Krista (waliyi) na Rom, wanda shi ne mutum mai girma a can bayan tafiyar sarkin…… Ikklesiyar Rom ta wannan hanya ta sanya kanta a asirce cikin masayin Romawa na mulkin duniya, wanda ita tana cin gaba ne na siyasa, kuma tana kafa kanta a masayin mulkin duniya, domin ta ci gaba ne na mulkin Romawa. Paparoma, wanda yana kiran kansa sarki da kuma firist na ***makzenus (pontifex maximus),*** shine magajin Kaisar." *Adolf Harnock, what is Christianity? 1903, PP. 269-270*

"gama ruhohin aljanu ne su, masu-aika alamu; suna kwa fita zuwa wurin sarakunan dukan duniya, garin su tattara su zuwa yakin babbar rana ta Allah Mai-iko duka." Ruya 16:13-14.

"Amma Ruhu yana fadi a sarari cikin kwanaki na karshe, wadansu zasu ridda daga imani, suna maida hankali ga ruhohi na rudami da na koyaswar aljanu. Ta wurin riyar mutane masu-fadin kariya,

**Ka lura da wadannan takalidai(al'adu) na ikklisiyar Katolika da kuma shekaran da suka fara:**

**A.D. 300:** Adu'o'i don matatuda alamar giciye.
**321:** tilasta dokoki na kiyaye Lahadi.
**375:** Daukaka mala'iku da kuma matattun tsarkaka, da kuma amfani da gumaka.
**394:** Yin hidima na mass na arna.
**400:** Sananci na masu kiyaye Assabbat na Litafi Mai-Tsarki ya fara.
**431:** Daukaka Maryamu, kamar yadda ake kiranta "Uwar Allah."
**450:** Hukunci na kisa akan masu kiyaye Assabbat.
**500:** Suturce firistoci da bam.
**536:** Koyaswa na zuwa wani wuri bayan mutuwa (purgatory).
**600:**Yin amfani da harshe Romawa kadai a sa'ar adu'a, da sujada da kuma yin adu'a ta wurin Maryamu da tsarkaka da mala'iku.
**607:** Amfani da sunan paparoma da Limamin Krista na duniya.
**709:** Yi ma kafafuwan paparoma sumba.
**786:** Sujada na giciye, da gumaka da aljanu da kasusuwa.
**927:** Kolejjin yan majalisan paparoma.
**965:** Baptisman kararawa.
**995:** Shafe matattun tsarkaka.
**998:** Azumi na juma'a da kuma lokacin Lent.
**1079:** Rashun auren firistoci.
**1090:** Rosali da kuma adu'ar hanu da cazbi.
**1184:** Kotun tuhuma.
**1190:** Sayar da nishaddai (gafara).
**1215:** Furta zunubai ga jin firis a madadin Allah.
**1220:** bangirma ga gurasar jibi
**1229:** hana jama'a Littafi Mai-Tsarki.
**1251:** Skafula. (Scafular).
**1414:** An hana jama'a kokon.
**1508:** Ana furta Ave mariya da cazbi.
**1524:** An kafa kungiyar mayakan Asiri na Katolika.
**1545:** An shelata takalidai na Afokrifa.
**1854:** An shelata daukan juna biyu na maryamu a cikin jiki mara zunubi.
**1864:** "Tsarin kuskure" na Paparoma, hana yancin adini, da furci,da lamiri, da rubutu, da dukan kirkirowa na kimiyya.
**1870:** Rashin kuskure na paparoma.
**1930:** Haramtar da makarantu na jama'a (gwamnati) da na wadanda ba Katolika ba ne.
**1950:** An shelata korafin budurwa Maryamu.
**1965:** An nadda Maryamu uwar Ikklisiyoyi: na almajirai maza , da mata, damasu kebe kai, da makarantu horaswa, da lent, da makomai tsarki, da Lahadin garin dabino, da ruwa mai-Tsarki, da Larabar toka, da Ranar dukan tsarkaka, da ja-jibirin ranar dukan tsarkaka, da ranar kifaye, da ranar sumagiya (bulala), da kona turare, da mai-tsarki, da Alamar martaba, da jan hankali, da dai sauransu.

wadanda an yi ma lamirinsu lalas sai ka che da karfe mai-wuta." Timothawus ta 2, 4:1-2.

Dukan wandada suka ki yarda da dokan nan, za a razanar da su da tara, da hukuncin kurkuku da kuma mutuwa karshe.

"Har kuma shi sa a kasha iyakar wadanda ba suyi sujada ga gumkin bisan ba." Ruya 13:15.

Wannan doka ta kiyaye ranar Lahadi za a zatas da ita a kasar Amirka ne, sa'annan kowane kasa a bisa doron duniya zata bi baya-tsohon Meziko, Amirka ta kudu, Indiya, Asia, Turai, Roshiya, Africa da kuma dukan sibirai na teku. Kowane mutum a cikin dukan duniya dole ya dauki kuduri ko ya yi biyaya ga dokar Allah, ko dokar mutane.

"Dukan mazamnan duniya kuma za su yi masa sujada, kowane wanda ba a rubuta sunansa tun kafawar duniya a chikin Littafi rai na Dan-rago wanda aka kasha ."Ruya 13:8. "Hayakin azabarsu kuma yana hawa har zuwa zamanun zamanai; ba za su kwa da hutu dare da rana, su wadanda ke yin sujada ga bisan da gumkinsa, da iyakar wanda ya karbi shaidar sunansa." Ruya 14:11.

**Zamu iya yin tambaya, yaya ne mulkin Rom ta Paparoma ta zo ga samun wannan iko mai-yawa?**

"ya (na)tsaya kuma bisan yashi na teku. Na ga-

Shaidar bisan. Zasu karbi aloba bakwai na karshe. "Na farin ya tafi, ya zuba nasa kasko chikin duniya; sai ya zama mugun gyambo mai-azaba bisa mutane wadanda suke da shaidar bisan, masu-sujada ga gumkinsa kuma." Ruya 16:2.

Akwai Krista na gaskiya a cikin kowane ikklesiya, har da ikklesiyar katolika, wanda sun yi ma Allah sujada ran Lahadi. Sun yi rayuwa ne ga dokan haske da sun samu. Sun bauta ma Allah zuwa kadadan saninsu. Basu karbi **SHAIDAR BISAN** ba. Amma sa'anda za a tilasta kiyaye **LAHADI** ta wurin doka, a wacan lokacin, dukan wanda zai yi biyaya ga dokoki na mutane ya ki dokar Allah, zai karbi-

## *Hatimin Allah*

Ba duka ba ne za su karbi shaidar bisan:

" Na ga kuma sai ka che teku na madubi garwaye da wuta; da wadanda suka tafo masu-nasara da bisan, da gumakinsa da nomba na sunansa, suna tsaye a bisa teku na madubi, suna da girayu na Allah." Ruya 15:2.

Wadanda ba su karbi shaidar bisan ba, zasu karbi hatimin Allah.

"Ya ce, kada ku chiwuchi kasa, ko teku, ko itatuwa tukuna, sai mun hatimchi bayin Allahmu bisan goshinsu." Ruya 7:3.

"Ka damre shaidan, ka hatimche shari'a a wurin almajiraina." Ishaya 8:16.

Hatimin Allah tana bayana **SUNA, DA IKO DA KUMA MALLAKAR MULKI** na Allah a cikin dokarsa Mai-Tsarki:

"Ka tuna da ranar assabbat, domin a kiyaye ta da tsarki. Kwana shidda za ka yi aiki,ka kwa gama dukan aikinka: amma rana ta bakwai assabbat ne ga Ubangiji, Allahnka: cikinta ba za ka yi kowane aiki ba, da kai, da danka, da diyarka, da bawanka, da bisashenka, da bakonka wanda ke chikin kofofinka: gama chikin kwana shidda Ubangiji ya yi sama, da kasa, da teku, da abinda ke chikinsu, ya huta kuma a kan rana ta bakwai: domin wannan Ubangiji ya albarkaci ranar assabbat ya tsarkaketa." Fitowa 20:8-11.

"Alama che tsakanin ni da yayan Isra'ila har abada:gama chikin rana ta bakwai ya huta, ya lumfasa." Fitowa 31:17.

"Ku tsarkake assabbataina; za su zama shaida tsakanina da ku, domin ku sani nine Ubangiji Allahnku." Ezekiel 20:20.

Assabbat na rana ta bakwai har yanzu ranar Allah ce mai tsarki kuma biyaya ga dokar Allah itace gwajin karshe na **HATIMIN ALLAH**.

"Na ga kuma wani mala'ika yana tashi daga wurin fitowar rana(gabas),….ya che, kada ku chuchi kasa, ko teku, ko itatuwa tekuna, sai mun hatimchi bayin Allahnmu bisa goshinsu." Ruya 7:2-3.

"Gama yadda sabobin sammai da sabuwar duniya, wadanda zan yi, za su dawama a gabana, in ji Ubangiji, hakannan kuma zinariyarku da sunanku zasu dawama.

"Za ya zama kuma, daga wani sabon wata zuwa wani, daga wata assabbat kuma zuwa wata assabbat dukan masu-rai za su zo su yi sujada a gabana, in ji Ubangiji." Ishaya 66:22-23

"Ina chikin Ruhu a kan ranar Ubangiji." Ruya 1:10.

**Menene ranar Ubangiji?**

"Ya che masu, Dan mutum Ubangijin assabbachi ne." Luka 6:5.

Ranar Ubnagiji itace rana ta bakwai ga mako:Ranar Assabbat .

An bada foto na dokar (umurni) na kiyaye lahadi a matsayi na yaki ne akan mutanen Allah.

"Sai dragon ya hasala da gaske da machen, ya tafi domin shi yi yaki da sauran zuriyanta, wadanda su ke kiyaye da dokokin Allah, suna rike da shaidar Yesu." Ruya 12:17.

"Masu albarka ne wadannan da ke wankin tufafinsu (ko, da ke kiyaye dokokinsa)**KJV** domin su sami iko su zo wurin itachen rai, su shiga kuma ta kofofi chikin birni." Ruya 22:14.

Ikklisiyoyi da yawa, da kuma wadansu hanyoyi na sujada ba su a cikakken biyaya da Littafi Mai-Tsarki. Suna garwaye gaskiya da takalidai na arna da mutane.

"Amma a banza ne su ke yi mani sujada, koyaswa da su ke yi dokokin mutane ne." Matta 15:9.

Kiyaya Lahadi takalidi ce mutane. Ya zo ne daga arna masu bautan rana. Koyaswar rashin mutuwar rai ba daga littafi Mai-Tsarki ba. Baptismar na jarirrei ba a koyasda ita a Litafi Mai-Tsarki ba. Babtismar yayya-fawa ba daga Littafi Mai-Tsarki ba ne.

"Mu yayan Katolicka, muna da izini daya ne na kiyaye Lahadi da tsarki, a madadin Sati, kamar yanda muke da shi game da kowane bangaren koyaswarmu, a bayane, izini na ikklesiya. Amma wani takamammen izini ko kadan domin babu izini domin ta (kiyaye ranar Lahadi) a cikin Littafi Mai-Tsarki.kuma ba za ku che akwai izini domin ta a wani wuri da bam ba. Dukan mu da ku, gaske muna bin takalidine game da wannan zance; amma muna bin ta da bangaskiya cewa ita bangaren kalmar Allah ne, kuma ikklisiyar katolika ne Allah ya sanya ta ta tsare ta kuma fasara ta; kuma bin ta (ikklisiyar katolika), kuma zarginta a dukan lokaci da cewa tana kuskure tana kuma jagoranta a mummunnan hanya, ta wurin mayar da dokokin Allah wofi (Matta 15:6). *The Brotherhood of st. Paul, "The Clifton Tracks" vol. 4, track 4, P.*

"Daidai ne a tunas da presbiteriyawa, Da yan baptisma, Da yan tsarki (Methodists) da kuma dukan Krista, ka cewa Littafi Mai-Tsarki bata goyi bayan su a wani wuri ba game da kiyaye Lahadinsu. Ikklisyar Rom ta katolika ne ta kafa Lahadi, kuma wadanda suna kiyaye ranar suna kiyaye doka ce na ikklisiyar katolika." *Priest Brody in an address reported in Elizabeth, N,J, Newsof March 18, 1903.*

### IKKLISIYOYIN DA SU KA KI IKON PAPAROMA SUN YARDA

Shugabanin adini, yan makaranta, da sananun ma –rubuta da dukan (mawallafa) wadanda babu shaka sun kiyaye Lahadi game da zancen al'ada ta ikklisiya; duk da haka sun bada shaidar goyon baya da cewa Assabbat na Littafi Mai-Tsarki, itace na rana ta bakwai ga mako (Sati) amma ba lahadi ba. Lahadi ba itace ranar Ubangiji ba.

### IKKLISIYOYIN DA SUKA KI IKON PAPAROMA SUN FURTA

**Masu tattaruwa (kongirgeshonalis):** "Yana nan a tsarari da cewa komin hima da mika kan mu wajen adana Lahadi, ba Assabbat muke kiyayewa ba…Assabbachi ta kafu ne akan dokar Allah na musamman, ba zamu iya samun irin wannan dokan domin kiyaye Lahadi ba….ko layi guda daya a cikin sabon-alkawali wanda ta bada ra'ayi na cewa, zamu fuskanci wata ta wurin ketare zato na tsarkin ranan Lahadi." *Dr R.W Dale. "The Ten commandmens," P. 106-107.*

**Yan ikklisiyar yanci na Luduran (Lutheran):** gama sa'anda ba za a iya tanada wani nasi guda daya a cikin Littafi Mai-Tsarki wanda ta shaida cewa ko Ubangiji da kansa ko kuma manzanensa, sun umurta irin wannan sakewa daga Assabbat zuwa Lahadi, ba zai kasance abu mai saukin amsa ba: wanene ya sake Assabbat, kuma wanene ya taba samun izini (dama) na yin haka? "*George Suerdrup, A New Day*"

**Priesbiteriyawa**: babu wani, ko alama a cikin Sabon-Alkawali game da janyewa daga aiki akan ranan Lahadi. Kiyaye Larabar toka, suna tsaye ne akan matsayi daya da kiyaye Lahadi. Game da hutu Lahadi babu wani dokar Allah da ta shiga. *Cand Eyton, in "The Ten Commandments."*

**Angilika**: kuma a ina ne an kafa mana cikin Littafi Mai-Tsarki cewa muna kiyaye rana ta fari ko kadan? An dokace mu mu kiyaye rana ta bakwai; amma babu inda aka dokace mu mu kiyaye rana ta fari." Isaac *Williams "Plai Sermon on the Catechism" PP. 334, 336.*

**Yan tsari (metodis):** "Gaskiya ne babu wani doka na goyon baya game babtismar jarirai. Kuma babu wani game da kiyaye rana ta fari ga mako. Yawanci sun gaskanta cewa cristi ya sake Assabbat. Amma, daga kalmomin bakinsa, mun gan cewa baya zo domin wata manufa kamar haka ba. Wadanda sun gaskanta da cewa yesu ne ya sake Assabbat suna danganta shi akan zato

ne kadai" Amos Binney, Theological compendium, pp, 180-181.

**Afiskofaliya**: mun sake daga rana ta bakwai zuwa rana ta fari, daga sati zuwa lahadi, akan izini na makadaiciyar mai tsarki, katolika, ikklisiyar manzanai na Kristi "*Bishop Seymour, "Why we keep Sunday.*"

**Yan babtisma(Baptist):** "Babu shakka na sani a tsarari cewa, an fara anfani da lahadi a tahirin Krista nafari kamar ranar adini, kamar yanda mun koyo daga Babani na Krista da wadansu rubuce-rubuce amma abun tausayin shine ya zo cike da hadi na shaidar arnanci(al'ummanci), kuma an kristance shi da sunan allahn-rana, sa'annan an karba an tsarkake tawurin riddan mulkin paparoma, an kuma mika a matsayin tsatsarkar gado zuwa ga ikklisiyoyin da suka ki ikon paparoma "*Dr. E.T Hiscox, report of his sermonat the Baptist ministers convention, in new york Examiner, November16,1897.*

Mun rigaya mun bada maganganu dayawa daga rubuce-rubucen katolika wadanda sun bayana a tsarari da cewa itace ta sake Assabbsat daga ranar sati, ranar ta bakwai zuwa ranar lahadi, rana ta fari ya mako. Sun kuma tabbatar da cewa sune sun kawo sujadan ranar lahadi cikin iklisiyar Krista domin dukan mutane su kiyaye.

Mun rigaya mun bada maganganu daga shugabanin ikklisiyoyin da su ka ki ikon paparoma da kuma sanannun marubuta (ma wallafa), wadanda sun fito a fili sun fada cewa babu wani wuri a tsohon alkawali na litafi mai tsarki da za'a sami aya daya don sujada ranar lahadi ko kuma don tsarkake ta ranar lahadi.

Lahadi bata da tsarki. Lahadi kamar rana na sujada ta zo ne daga arna masu bautan-rana.

**"Don me kuma kuna ketare dokar Allah saboda takalidinku?**...ku masu riya, daidai Ishaya ya yi anabci a kanku, da ya ce, wannan al'umma tana girmamana da lebunansu; amma zuciyarsu tana nesa da ni. Amma banza suke yi mani sujada, koyaswa da suke yi dokokin mutane ne..." "Amma ya amsa, ya ce, kowane dashe wanda Ubana na sama ba ya dasa ba, za a tumbuke shi." "Ku bar su: majayan hanya ne makafe. Idan makafo ya ja ma makafo gora, duka biyu zasu fada cikin rami." Matta 15:3, 7-9, 13-14.

Kashedi na karshe game da shaidar bisan zaya zama sako na dukan duniya. Za a kai sakon ta wurin Radio, telebijin da jaridu a kowane kasa ta duniya. Allah zaya ba kowane mutum zarafin zabe na karshe, biyayya gareshi, ko kuwa biyayya da dokokin mutane, wanda ke sabani da dokokin Allah.

"Bayan wannan na ga wani mala'ika yana sabkowa daga sama, yana da hukunci da yawa; duniya kuma ta haskaka domin daukakarsa."

"Ya tadda murya da karfi, ya ce, fadadiya ce, fadadiya ce Babila babba, ta zama gidan aljanu, da madamrar kowane kazamin ruhu da kowane kazamin sunsu mai ban kyama. Gama da ruwan anab na hasalar fasikancinta dukan al'ummai sun fadi; sarakunan duniya kuma suka yi fasikanci tare da ita, dillalan duniya kuma suka wadata bisa ga ikon annishuwanta."

" Na ji wata murya daga sama, ta ce, ku fito daga cikinta, ya al'ummata, domin kada kuna tarayya da zunubanta, kada ku sha rabon alobanta: gama zunubanta sun kawo har ga sama, Allah kwa ya tuna da muguntanta."

"Ku saka mata kamar yadda ta bayas, ku saka mata gwalgwadon ayukanta, ribi biyu: cikin koko wanda ta dama, ko dama mata sau biyu."

"Domin wannan fa, rana daya alobanta za su zo, mutuwa da kewa, da yunwa; za a koneta sarai da wuta; gama Ubangiji Allah Mai-karfi ne wanda ya sharanta mata." Ruya ta Yohanna 18:1-6, 8.

"Sarakunan duniya kuma, da hakimai, da jarumawa, da attajirai, da masu karfi, da kowane bawa da da, suka buya chikin ramumuka da pannun duwatsu; suna ta ce ma duwatsu da pannu, ku fado mana, ku rufe mu daga fuskar wanda ya zamna bisa kursiyin, daga hasalar Dan ragon kuma; gama babbar rana ta hasalarsu ta zo; wa ke da iko shi tsaya kuma?" Ruya ta Yohanna 6:15-17.

"Na ga Bisan kuma, da sarakuna na duniya, da rundunan yakinsu, a tattare domin su yi yaki da wadanda yake zamne bisa dokin, da rundunansa kuma."

"Aka kama bisan; tare da shi kuma mai-karyan anabci, wanda ya kan aika alamu a gabansa, irin da ya kan rude masu karban shaidar bisan da wadanda ke sujda ga gumkinsa: aka jefa su biyu da rai chikin korama ta wuta mai ci kibiritu." Ruya ta Yohanna 19:19-20.

"A ran nan fa za a ga kisassun Ubangiji tun daga wannan iyakar duniya zuwa wannan iyaka: ba za a yi makokinsa ba, ba za a tattara, ba kwa za a bizne su ba: zasu zama taki a fuskar kasa." Irmiya 25:33.

## Allah Zaya Lura Da Dukan Wadanda Suna Dogara Da Kuma Biyayya Da Shi

Ba za ka ji tsoron razanar dare ba; ko kwa kibiya wanda ke tashi da rana: ko aloban da ke yawo a chikin dufu, ko hallaka wanda ke lalataswada tsakar rana.

"Mutum dubu za su fadi daura da kai. Zan bar goma kuma a hannunka na dama; amma ba za ta kusance ka ba.....

"Gama kai ne mafakata, ya Ubangiji! Ka maida madaukaki wurin zamanka; babu mugunta da za ta same ka, babu wata aloba da za ta kusance tent naka." Zabura 91:5-7, 9-10.

"Bayan wannan na ga mala'iku fudu suna tsaye a wajen kusuruwoyi fudu na duniya, suna rike da iskoki fudu na duniya, domin kada kowane iska ya hura bisa kasa, ko teku, ko bisa kowane itace.

"Na ga kuma wani mala'ika yana tashi daga wurin fitowar rana, yana rike da hatimi na Allah Mai-rai:ya tada murya da karfi ga mala'iku fudu din, wadanda aka sanya masu su chuci kasa da teku,

"Ya ce, kada ku chiwuci kasa da teku, ko itatuwa tukuna, sai mun hatimci bayin Allahnmu bisa goshinsu." Ruya ta Yohanna 7:1-3.

"Ba za su kara jin yunwa ba, ba kwa za su kara jin kishin ruwa ba, rana kuma ba za ta buge su ba, ko kowane irin zafi;

"Gama Dan-rago wanda ke cikin tsakiyar kursiyin za ya zama makiyayinsu, za ya bishe su kuma wurin mabulbulan ruwaye na rai: Allah kuma za ya share dukan hawaye daga idanunsu." Ruya ta Yohanna 7:16-17

"Ku zo, mutanena, ku shiga cikin dakunanku, ku rufe ma kanku kofofi: ku buya kadan, har fushin ya wuce.

"Gama, gashi Ubangiji yana fitowa daga wurinsa domin shi yi ma mazamnan duniya hukunci saboda muguntansu. Kasa kuma za ta bude asirin jininta, ba kwa za ta kara rufe kisassunta ba." Ishaya 26:20-21.

"Na ga wata alama kuma chikin sama, babba ce mai ban al'ajibi kuma, mala'ika bakwai suna da aloba bakwai, na karshe ke nan, gama a cikinsu hasalar Allah ta cika.

"Na ga kuma sai ka ce, teku na madubi garwaye da wuta; da wadanda suka tafo masu-nasara da bisan, da gumkinsa, da nomban na sunansa, suna tsaye a bisa teku na madubi, suna da girma na Allah.

"Suna raira waka ta Musa bawan Allah, da wakar Dan-rago, suna cewa, ayukanka masu girma ne, masu ban al'ajibi, ya Ubangiji Allah, mai-iko duka; hahalullukanka kuma masu-adilci ne, masu-gaskiya kuma, ya sarkin zamanai." Ruya ta Yohanna 15:1-3.

"Sai dragon ya hasala da gaske da matchen, ya tafi kuma domin shi yi yaki da sauran zuriyanta, wadanda suke kiyaye da dokokin Allah, suna rike da shaidar Yesu." Ruya 12:17.

"A wannan lokaci fa, Michael (Mikailu) za ya tashi tsaye, shi babban sarki mai-kariyar yayar jama'arka; za a yi kwanakin wahala irin da ba a taba yiba tun da aka yi al'umma har loton nan; a loton nan kwa za a ceci mutanenka, kowane daya wanda aka iske shi a rubuche cikin wadanda suke barci cikin turbayar kasa za su falka, wadansu zuwa rai na har abada...." Daniel 12:1-2.

"A tsakiyar jijjiguwar duniya, da walkiya, da rurin sawa, muryar Dan Allah ya kira matattun da ke barci cikin Kristi. Ya dubi kabarbaru na tsarkaka, sai ya daga hannu sama,ya yikira da karfi, 'ku falka, ku falka, ku falka, ku da kuke barci cikin turbayar kasa, ku tashi'....Daga cikin kabarbaru za su fito yafe da jiki mara mutuwa mai daraja, suna cewa 'ya mutuwa, ina nasaranki (karinki)? Ya mutuwa (kabari), ina nasaranki?" 1 Korintiyawa 15:55. "Babban Hargitsi, shafi na 644.

"Gama Ubangiji da kansa za ya sabko daga sama, da kira mai-karfi, da muriyan sarkin mala'iku, da kafon Allah kuma: matattu ka ke cikin Kristi za su fara tashi:

"Sa'annan mu da mu ke da rai, mu wanzu, tare da su za a fyauce mu zuwa cikin gizagizai, mu tarbe Ubangiji a sararin sama: hakanan zamu zama har abada tare da Ubangiji." 1 Tassalunikawa 4:16-17.

"Mai-shaidan wadannan al'amura ya ce, Hakika: ina zuwa da sauri, Amin: ka zo, ya Ubangiji Yesu." Ruya ta Yohanna 22:20.

"Mai-albarka, mai-tsarki ne shi wanda ya ke da rabonsa cikin tashi na fari.....amma za su zama Priests na Allah da na Kristi, za su yi mulki kuma tare da shi shekara dubu." Ruya ta Yohanna 20:6.

"Na ga sabuwar sama da sabuwar duniya kuma: gama sama ta fari da

duniya ta fari sun shude; teku kuma ba shi

" Na ga kuma birni mai-tsarki, sabuwar Urishalima tana sabkowa daga sama wurin Allah, shiryayya kamar amarya da ado domin mijinta.

"Na ji babbar murya kwa daga cikin kursiyin, ta ce, Duba, mazamnin Allah yana wurin mutane, za su zama al'ummai nasa, Allah kuma da kansa za ya zamna tare da su, ya zama Allahnsu.

"Za ya share dukan hawaye kuma daga idanunsu: mutuwa kwa ba za ta kara kasancewa ba; ba kwa za a kara yin bakin zuciya ba, ko kuka, ko azaba: al'amura na fari sun shude.

"Shi kuma wanda ke zamne bisa kursiyin ya ce, Duba, sabonta dukan abu ni ke yi. Ya ce kuma, ka rubuta: gama wadannan zantattuka masu aminci ne masu gaskiya." Ruya ta Yohanna 21:1-5.

"Sa'annan shi sarkin za ya ce ma wadanda ke hannun damansa, ku zo, ku masu-albarka na ubana, ku gaji mulkin da an shirya dominku tun kafuwar duniya." Matta 25:34.

## *Kamnar Allah*

**Yaya aka bayanna Allah?**

"Gama Allah kamna ne…." Yohanna 4:8.

**Yaya yawan kamnar Allah zuwa ga duniya?**

"Gama Allah ya yi kamanr duniya har ya bada Dansa haifaffe shi kadai, domin dukan wanda yana bada gaskiya gareshi, kada ya lalace, amma ya samu rai na har abada." Yohanna 3:16.

**Ta wace hanya na musamman ne kamnar Allah ta bayannu?**

"Inda aka bayanna kamnar Allah zuwa gare mu ke nan, Allah ya aike Dansa haifaffensa kadai cikin duniya, domin mu rayu ta wurinsa." 1 Yohanna 4:9

**Allah yana zuba albarkunsa akan mutane nawa ne?**

"Gama ya kan sa ranatasa ta fito ma miyagu da nagargaru, ya kan aiko da ruwa bisa masu adilci da marasa-adilci." Matta 5:45.

**Idan mun dubi kamnar Allah, menene zamu yi tsamani da gaba-gadi?**

"Wanda ba ya kebe Dansa ba, amma ya bashe shi domin mu duka, kaka za ya rasa ba mu abu duka kuma tare da shi a yalwace? "Romawa 8:32.

**A wace kalma guda daya ne an bayana halin Allah?**

"Wanda ba ya yin kamna ba, ba ya san Allah ba; gama Allah kamna ne." 1Yohanna 4:8.

**kamnar Allah zuwa ga yayansa zata dawama har zuwa wane lokaci ne?**

"Ubangiji ya bayana gareni tun daga nesa, ya ce, Hakika, na yi kamnarka da madawamiyar kamna: domin wannan na jawo ka da rahama."Irmiya 31:3

**Ko akwai abinda zaya iya raba dan Allah na gaskiya da kamnarsa?**

"Gama na kawas da shakka, ba mutuwa, ba rai, ba mala'iku, ba sarautai, ba al'amuran yanzu, ba al'amura na zuwa, ba ikoki, ba tsawo, ba zurfi, ba kwa wani halitacen abu, da za ya iya raba mu da kamnar Allah, wanda ke cikin Kristi Yesu Ubangijinmu."Romawa 8:38, 39.

**Zuwa ga wanene tsarkaka zasu yi ta raira yabo har abada?**

"... A gareshi wanda ya ke kamnarmu, ya kwance mu kuma daga zunubanmu cikin jininsa;—a gareshi daukaka da mulkin har zuwa zamanun zamanai."Ruya ta Yohanna 1:5-6.

**Yaya aka bayana juyayin da kuma jinkai na Allah?**

"Amma kai, ya Ubangiji, Allah ne cike da juyayi, mai-alheri kuma, maijinkirin fushi, mai-yawar jinkai da gaskiya." Zabura 86:15.

**Don menene Kristi ya ce mu kamnaci makiyan mu?**

"Amma ni ina ce maku, ku yi kamnar (makiyanku) magabtanku, kuma wadanda su kan tsananta maku, ku yi masu adu'a; domin ku zama yayan ubanku wanda ke cikin sama: gama ya kan sa ranatasa ta fito ma miyagu da nagargaru, ya kan aiko da ruwa bisa masu-adilci da marasa-adilci." Matta 5:44-45

## *Sa'ar Hukumcin Allah*

**Wane sako ne mai daukan hankali an bayas a Ruya ta Yohanna 14:7?**

"Ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja; gama sa'ar hukuncinsa ta zo: ku yi sujada ga wanda ya yi sama da duniya da teku da mabulbulan Ruwaye."

**Yaushe ne sa'ar hukumcin Allah?**

"Ya ce mani, Har yamma da sefiya gudu alfin da dari uku (dubu biyu da dare uku); kana za a tsarkake wuri mai-tsarki." Daniel 8:14. (ka dubi tsarin bayani)

**KA LURA**: Ranar kafara ta Yahudawa takan fadi a rana ta goma ga wata na bakwai, a wannan lokaci ne ake tsarkake haikali. Wannan rana ne, yahudawa suke maishe shi ranar shari'a ko hukumci, sa'annan shine kwatankwacin sharia ta bincike a sama. Shekaru 2300, bisa ga anabci, ya kai lokacin. Tsarkake haikali a sama, ko kwa shari'a ta bincike. Misali na Hadimar haikali yahudawa ya samu cika ne a cikin aikin Kristi kamar yanda ranar kafara na zamarin da daidai ne da ranar sharia, hakanan ne aikin Kristi ya kunshi shari'a ta binciken rayukan mutanensa kafin dawowar sa don ya karbe su zuwa wurinsa.

**Wace tabaci ne muke da shi cewa akwai sharia?**

"Allah… ya sanya rana, inda za ya yi ma duniya duka shar'ia." Ayukan Manzanic 17:30-31.

**Ko da shari'a tana tukuna ne a zamanin Bulus?**

"Yana bubbude zancen adalci, da kamewa, da shari'a mai zuwa…." Ayukan Manzani 24:25

**Daga cikin menene za'a yi ma dukan mutane shari'a?**

"Aka bude Litatafai: aka bude wani Litafi kuma, Latafin rai ke nan: aka yi ma matattu shari'a kuma bisa ga abin da aka rubuta cikin Litatafai, gwalgwadon ayukansu." Ruya ta Yoh.20:12. "Ku ji tsoron Allah, ku ba shi daraja, gama sa'ar hukuncinsa ta zo." Ruya ta Yoh.14:7.

**KA LURA**: Litafi ya ambaci sassa uku na shari'an: shari'a ta Bincike, wanda zai yi kafin zuwan Yesu na biyu; shari'an da Kristi tare da tsarkaka zasu yi ma duniyan da ta bata, da malaikun shaitan a lokacin shekaru dubun da zasu bi bayan zuwan Yesu na biyu. Da kuma sharia ta aiwatar da hukumci bisa miyagu a karshen shekaru dubun. Shari'a ta Bincikin za'a yi ta a sama ne kafin Yesu ya sake dawowa, don ya tabbatar da wadanda sun cancanta tashi na fari, da kuma canji kamar da kyaptar ido, a lokacin karar kafo na karshe. Ya zama wajibi wannan ya faru kafin zuwansa na biyu domin babu lokacin yin haka in ya zo, a lokacin tashin matattu na masuadilci. Aiwatar da hukumcin miyagun za ya faru ne bayan an riga an bincike ruhoton rayuwan su lokacin shekaru dubu a sama. (dubi Ruya ta Yoh. 20:4-5; 1korintiyawa 6:1-3). Sakon malai'ka na Ruya ta Yohanna 14:6,7 shine baton sharia ta Binciken.

**A matsayinsa na masakaici na mutanensa, menene Kristi zaya furta a gaban uban da mala'ikunsa?**

"Wanda yayi nasara za a yafe shi hakannan da fararren tufafi, ba ni kwa shafe sunansa daga cikin litafin rai ba dadai, zan kuma shaida sunansa a gaban ubana, da gaban mala'ikunsa."Ruya ta Yoh.3:5(dubi matta 10:32-33; markus 8:38.)

**KA LURA:** A lokancin wannan sharia, dukan matattu masumugunta da masu adilci zasu kasance a cikin kabarbarunsu. Lisafin ruhoton ruguwan kowane mutum yana nan a rubuce cikin Litatafai na sama.

## *Zuwan Yesu Na Biyu*

**Wane alkawali ne Kristi yayi game da sake dawowar sa na biyu?**

"kada zuciyar ku ta batci, kuna

### YIN SUJADA A EKKILISIYA TA GASKIYA (KO KUMA A GIDAJE)

Wannan yar takarda tana bada sako cewa duniyarmu musanman adinin Krista, bada dadewa ba zata fuskanci doka a duk duniya wanda zata bukaci barin dukan aiki a kan ranar Lahadi (wato rana ta farko ga mako) da kuma yin sujada a wannan ranar da Papa Roma ya kafa ba tare da goyon bayan Litafi Mai-Tsarki ba.

Idan ka yarda da wannan ranan da sujadan, zaka karbi hatimi mai ban tsoro watau shaidan Bisan a bisa goshin ka. Amma idan kayi sujada ga Allah akan ranarsa ta bakwai ga mako, (watau ranar assabar) ranar da tana tuna mana da ikon Allah na halitta kamar yadda aka bayyana mana a doka ta hudu cikin tsarin dokokin Allah ga dukan duniya (Fitowa 20:8-11), (Farawa 2:1-3), zaka karbi kyakyawar hatimin Allah bisa goshinka ka kuma samu rabon kasancewa da Allah har abada. Ikkilisiyoyi dayawa, da Limamai da dumbin jama'a, suna juyawa zuwa kalmar Allah kamar yadda aka bayyana a cikin wannan yar takarda, kuma suna daukan matsayinsu gabagadi domin biyayya ga umurnin Allah. Bayan ka bayyana wannan sako ga Ekkilisiyar ka, idan sun ki yin wa'azin ta, muna baka shawara ka raba kanka da Babila (Ruya ta Yohanna 18) ta wurin yin sujada a Ekkilisiya na gaskiya ko kuma a gidanka. Ka gayaci iyali, abokai da kuma makwabta har ga kafawan kanannan Ekkilisiyoyi na wadanda bangaskiyanku ya zo daya daomin ku zama musu rufa ko, cika gibin da aka sa cikin dokokin Allah guda Goma. Da haka zaka iya karban alkawalinKristi. "Gama wurin da mutum biyu ko uku sun taru chikin sunana, nan ni ke a tsakiyarsu." Matta 18:20.




Lokachin anabcin mafiya amfani (ma'ana) Shekaru 2300 din zai kai (150) "fitowar doka a maida Urishlima , a gina ta kuma;" bisa ga anabcin Daniel (Daniyelu) zuwa ga lokacin da za a tsarkake wuri mai-tsarki (haikali).

**B.C.457—**Artaxerxes, Sarkin Pashiya (Persia), ya bada umurni (doka) na mayas wa da sake ginin Utishalima din (Daniel 9:12). Farkon shekaru 2300 din kenan.

**B.C 408—**An gama ginawa da mayas da Utishalima. A cikin (lokacin) shekaru 49 na farkon anabcin Daniel (Daniyelu) mai tsawo na kamala aikin a shekara ta B.C 408.

**A.D. 27—**An shafe Yesu da Ruhu Mai-Tsarki a lokacin babtismar sa, ya fara wa'azi da koyaswa. Duba Matta 3:16; Ayukan Manzani 10:38. Daga B.C 457. zuwa ga Kristi "shafaffe: shekaru 483.

**A.D. 31—**Masiya (shafaffe, ko Kristi) a "tsakiyar bakwai din (mako daya) an dasse shi, A.D. 31, bayan shekaru uku da rabi ($3^1/_2$) shekaru na hidimar sa mai albrka. Duba

bada gaskiya ga Allah. Ku bada gaskiya gareni kuma. A cikin gidan ubana akwai wurin zama da yawa; da ba haka ba, da na fade maku; gama zan tafi garin in shirya maku wuri. Kadan na tafi na shirya maku wuri kuma, sai in sake dawowa, in karbe ku wurin kaina; domin wurin da ni ke, ku zamna kuma." Yohanna 14:1-3

**Menene zaya bi bayan cikan alamun zuwan Yesu?**

"sa'annan zasu ga Dan mutum yana zuwa a cikin girgije tare da iko da babbar daraja." Luka 21:27.

**Ko baton salama a duniya zata yaudari jama'a a cikin tsaro ta yamusai?**

"Kun san wannan da fari, cikin kwanaki na karshe masu-ba'a za su zo da ba'a, suna bin nasu sha'awowi, suna cewa, ina alkawalin tafowassa? Gama tun daga randa ubanni suka kwanta barci, dukan al'amura suna nan kamar yadda su ke tun farkon halita." 2Bitrus 3:3-4

"Gama ku da kanku kun sani sarai ranar Ubangiji tana zuwa misalin barawo da dare. Suna cikin fadin, kwanciyar rai da lafiya, sai ga hallaka farap ta abko masu…. Amma ku, yan uwa, ba cikin dufu kuke ba, da ranan nan za ta tarshe ku kamar barawo." 1Tasalunikawa 5:2-4.

**A tafiyarsa zuwa sama, yaya ne an alkawarta sake dawowarsa?**

"Tun suna cikin zuba ido zuwa sama, yana tafiya, sai ga mutum biyu daura da su a tsaye da fararen tufati. Suka ce kuma, ku mazajen Galili, don me kuke tsaye kuna duba zuwa sama? Wannan Yesu wanda aka daukeshi daga wurinku, aka karbe shi sama, kamar yanda kuka ga tafiyatasa zuwa cikin sama, hakanan za shi dawo." Ayukan Manzani 1:10-11.

**Ko mazamnan duniya dukan ne zasu kasance a shirya domin saduwa da Kristi?**

"Ga shi, yana zuwa tare da gajimarai, kowane ido kuma za ya ganshi, da su kuma wadanda suka soke shi, dukan kabilan duniya kuma za suyi bakinciki a kansa. Hakanan ne. Amin." Ruya ta Yoh.1:7

"Sarakunan duniya kuma, da hakimai…..suna ta ce ma duwatsu da pannu, ku fado mana, ku rufe mu daga fuskar wande ya zamna bisa kursiyin, daga hasalar Dan Rago kuma."Ruya ta Yoh.6:15-16

**Ko zuwan Yesu zai zama lokacin bada sakamako?**

"Gama dan mutum za ya zo cikin darajar ubansa, tare da malaikunsa; sa'anan zaya saka ma kowane mutum gwalgwadon aikinsa." Matta 16:27

"Ga shi, ina zuwa da samri; hakina yana tare da ni kuma, da zan saka ma kowane mutum gwalgwadon aikinsa."Ruya ta Yoh.22:12.

**Zuwa ga su wanene an yi alkawarin ceto a dawowar Yesu na biyu?**

"Hakanan kuma Kristi, bayan da aka mika shi so daya domin shi dauki zunuban mutane dayawa, zaya sake bayanuwa, banda zunubi, ga wadanda suke sauraronsa, zuwa ceto." Ibraniyawa 9:28

**Ta yaya ne wannan begen ya shafi wannan rayuwa?**

"Masoya, yanzu yayan Allah mu ke, kuma ba'a bayana ba tukuna yanda za mu zama. Mun sani, kadan am bayana shi, mu za mu zama kamansa; gama zamu ganshi kamar yanda shike. Dukan wanda yana da begen nan a kafe bisa gareshi ya kan tsarkake kansa, kamar yanda shi tsartsarka ne." 1Yohanna 3:2-3.

**Yaushe ne manzo Bulus zaya karbi rawaninsa?**

"Saura, an ajiye mani rawanin adilci, wanda Ubangiji, adilin mai-shari'a, za ya ba ni a **wannan rana: ba kwa ni kadai ba, amma dukan wadanda sun kamnaci bayanuwansa."** 1Timotawas 4:8.

## *Yanda Kristi Zaya Dawo*

**A lokacin tafiyarsa, yaya ne mala'ikun sun ce zaya sake dawowa?**

"sa'anda ya fadi wannan, su suna cikin dubawa, aka dauke shi bisa; girgije ya karbe har ya bace ma ganinsa. Tun suna cikin zuba ido zuwa sama, yana tafiya, sai ga mutum biyu daura da su a tsaye da fararen tufafi; suka ce kuma, ku mazajen Galili, don me ku ke tsaye kuna duba zuwa sama? Wannan Yesu wanda aka dauke shi daga wurinku, aka karbe shi sama, kamar yanda kuka ga tafiyatassa zuwa sama, hakanan za shi dawo."Ayukan Manzani 1:9-11.

**Yaya ne Kristi ya ce zaya dawo?**

"Gama Dan-mutum za ya zo cikin darajar ubansa tare da malaikunsa." Matta 16:27


"Sa'annan alama ta Dan-mutum za ta bayana a sama: sa'annan kuma dukan kabilan duniya za su yi bakin ciki, za su kwa ga Dan mutum yana zuwa a bisa gizagizai na sama tare da iko da daukaka mai-girma" Matta 24:30.

**Wane kashedi ne Yesu ya bayas game da koyaswoyin karya?**

"Sa'annan idan kowane mutum ya ce maku, Duba, ga Kristi nan ko kwa, ga shi nan; kada ku gaskanta. Gama masu-karyan Kristi zasu tashi, da masu-karyan annabci, za su gwada alamu masu-girma da al'ajibai kuma; har su badda ko zababu da kansu, da ya yiwu. Ga shi, na rigaya na fada maku tun ba ya yi ba. Idan fa sun ce maku, Ga shi yana cikin jeji; kada ku fito; ko kwa, Ga shi, yana cikin lolokai; kada ku gaskanta." Matta 24:23-26

**Ko ana iya ganin zuwansa?**

"Gama kamar yadda walkiya ta kan




Daniel 9:27; Matta 27:50-51. sauran shekaru uku Da rabin na bakwai-bakwai har saba'in, na saba'in din zai kawo mu zuwa karshen shekaru dari hudu da chasa'in (490) lokacin da an sanya ma mutanen Yahudawa.
**A.D. 34—**Jifar Istifanus. Daga wannan lokaci bisharan ta fara zuwa ga al'ummai. Duba Daniel (::24; Ayukan Manzani 7:54-58.;8:1. Daga B.C 457 ZUWA "zamanan al'ummai,". Shekaru 490. ko makoni saba'in (bakwai saba'in) ne.
**A.D. 1844—**SAKONI KASHI UKU NA Ruya 14:6-12. an shelata ga dukan duniya, dab da zuwan Kristi na biyu.
**A.D. 1844—**karshen shekaru 2300 kenan. Tsarkake wuri mai-tsarki (haikali) na sama a sa'arhukuncin Allah . duba Daniel 8:14; Ruya 14:7.

fito daga gabas, ana kwa ganinta har yamma; hakannan bayanuwa Dan mutum za ta zama."Matta 24:27.

**Me za ya faru idan kafo ta yi kara?**

"Gama Ubangiji da kansa za ya sabko daga sama, da kira mai-karfi, da muryar sarkin malaiku, da kafon Allah kuma: matattun da ke cikin Kristi za su fara tashi." 1Tasalunikawa 4:16.

**Wane irin rabe-rabe ne za'a yi?**

Amma sa'anda Dan-mutum za ya zo cikin darajarsa, da dukan malaiku tare dashi, sa'annan za ya zamna bisa kursiyin darajarsa: a gabansa kuma za'a tattara dukan al'umai: shi kwa za ya rarraba su da juna kamar yadda makayayi ya kan rarraba tumaki da awaki."Matta 25:31-32

**Me za ya ce ma wadanda ke hannun damansa?**

"Sa'annan shi sarki za ya ce ma wadannan da ke hannun damansa, ku zo, ku masu-albarka na ubana ku gaji mulkin da an shirya domin ku tun kafawar duniya." Matta 25:34

**Me za ya ce ma wadanda ke hannun hagunsa?**

"Sa'annan za ya ce ma wadanda ke ga hannun hagunsa, ku rabu da ni ku la'antattu, zuwa cikin wuta ta har abada, wadda an shirya ma shaitan da mala'ikunsa." Matta 25:41.

**Menene Ubangiji za ya zama ga mutanensa a wannan lokaci?**

"Ubangiji za ya yi ruri daga sihiyona, ya furtadda muryarsa daga Urushalima: samai da duniya zasu yi rawa; amma Ubangiji za ya zama mafaka ga mutanensa kakarfa wuri kuma ga yayan Israila."Joel 3:16 (duba Irmiya 25:30-31; Hagai 2:21; Ibraniyawa 12:26; Zabura 91:5-10.)

**Yaya ne Bulus yayi Magana game da zuwansa.?**

"Haka nan kuma Kristi, bayan da aka mika shi so daya domin shi dauki zunuban mutane da yawa, ga wadanda su ke sauraronsa, zuwa ceto." Ibraniyawa 9:28.

**Wace nassi ce ta yi Magana game da shekaru dubu?**

"Na ga kursiyai kuma, akwai mazamna a bisansu kuma, aka bada shari'a cikin hannuwansu…..suka rayu, suka yi mulki kuma tare da Kristi shekara dubu." Ruya ta Yohanna 20:4.

**Me za ya faru da masu-mugunta da suke da rai a lokacin zuwan Yesu na biyu?**

"Kamar yadda ya faru cikin kwanakin Nuhu kuma, hakannan za shi zama a cikin kwanakin Dan-mutum. Suna ci, suna sha, suna amre, suna amraswa, har randa Nuhu ya shiga cikin jirgi, ruwan rigyawa ya zo kuma, ya hallaka su duka. Kamar yadda kumar ya faru cikin kwanakin Lutu….Amma randa Lutu ya fita Saduma aka zuba wuta da kibiritu daga sama, aka hallaka su duka. Bisa ga wannan misalin za ya faru da kuma cikin rana da Dan-mutum za ya bayanu."Luka 17:26-30.

## *Farawan (Somawar) Shekaru Dubu*

**Tashin matattu nawa ne za'a yi?**

"kada ku yi mamakin wannan; gama sa'a tana zuwa, inda dukan wadanda suna cikin kabarbaru za su ji muryatassa, su fito kuma: wadanda sun yi nagarta, su fito zuwa tashi na rai; wadanda sun yi mugunta, zuwa tashi na shari'a." yohanna 5:28-29.

**Wane ajin mutane ne suna da rabo a tashin na fari?**

"Mai-albarka, mai-tsarki ne shi wanda yake da rabonsa cikin tashi na fari: mutuwa ta biyu ba ta da iko bisansu ba." Ruya ta Yohanna 20:6.

**Har tsawon wane lokaci ne za a**

### FARAWAN (FARKON) SHEKARU DUBU

1. Karshen aloba bakwai
2. Zuwan Kristi na biyu.
3. Matattu masu-adilci zasu tashi
4. Masu-mugunta zasu mutu, za a daure shaitan.
5. Masu-adilci zasu tafi sama.

### KARSHEN SHEKARU DUBU

1. Kristi da tsarkaku zasu sabko
2. Birni mai-tsarki zata sabko.
3. Matattu masu-mugunta zasu tashi
4. Za a kwance shaitan.
5. Za a halaka masu-mugunta.

Shekaru dubu shine zaya zama lokacin rufewar babban mako na lokacin Allah-Assabbaci ta shekara dubu ga duniya da kuma ga mutanen Allah; bayan kimanin shekaru dubu shida na tarihi dan adam.

Zaya bi bayan rufewar lokacin bishara, sa'annan zaya rigaye lokacin kafa madawamin mulkin Allah bisa duniya.

Zaya bayana abinda Littafi ya ce da shi, "Ranar Ubangiji." A farko da karshen al'amuran akwai tashin matattu.

Za a gane farawan shi ta wurin aloba bakwai na karshe, da zuwan Yesu na biyu, tashin matattu masu-adilci; daurewar shaitan da kuma fyaucewar tsarkaku zuwa sama;


Sa'annan rufewar shekaru dubu zaya nuna ta wurin sabkowar sabuwar birnin Urishalima, tare da Kristi da tsarkaku daga sama, tashin matattu masu-mugunta, kwancewar shaitan daga madamransa, da kuma hallakan masu-mugunta.

A lokacin shekaru dubu, duniya zata zama kango. Shaitan tare da mala'ikunsa ne za a barsu anan. Sa'annan tsarkaku tare da Kristi, zasu zamna domin yin shari'a bisa masu-mugunta, shirye-shirye domin hukunci na karshe bisansu.

Masu-mugunta zasu tashi; za a kwance shaitan na dan kankanin lokaci, sa'annan, shi tare da masu-mugunta zasu kewaye sansani na tsarkaku da kuma birni mai-tsarki. Sa'annan wuta daga sama, daga wurin Allah zata cinye su. Wutar da zata cinye masu-zunubi itace za ta tsakakke duniya nan. Duniyan da za a sabonta shine zaya zama mazamnin tsarkakku.

Shekaru dubu, daya ne daga cikin al'amura masu zuwa. Karshenta zata nuna farawan rayuwa ta sabuwar duniya.

# Ga Shi Yana Zuwa




**daure shaitan a wannan duniya?**

"Na ga wani mala'ika kuma yana sabkowa daga sama, yana rike da makublin rami mara-matuka, yana kwa da babbar sarka a hannunsa. Sai ya damki dragon, tsofon maciji, shi ne ibilis da shaitan, ya damre shi har zuwa shekara dubu, ya jefasda shi cikin rami mara-matuka, ya rufe bakin, ya sa masa hatimi a bisansa, domin kada shi kara rudin al'ummai har shekara dubu su cika." Ruya ta Yoahnna 20:1-3.

**Wane canji ne za a samu a yanayin shaitan a karshen shekara dubu din nan?**

"Bayan wannan sai a kwance shi domin kankanin lokaci." Ruya ta Yohanna 20:3.

**Matattu masu adilci za su falka a zuwan Yesu na biyu. To, yaushe ne za a tada masu-mugunta, watau sauran matattun?**

"Sauran matattu ba su rayu ba sai shekara dubu din suka cika tukuna." Ruya ta Yohanna 20:5

**Da zara an tadda masu-mugunta, menene shaitan za ya yi farap daya?**

"Sa'anda shekara dubu sun cikakuma, za a saki shaitan daga madamransa, za ya fito kuma garin ya rude al'umman da ke cikin kusurwoyi fudu na duniya, Gog da Magog, shi tattara su zuwa yakin; yawan su yana kama da yashi na teku." Ruya ta Yohanna 20:7-8.

**Don gaba da wanene miyagu za su yi shirin yaki, kuma menene za ya biyo baya?**

"Suka tafi kuma suka bazu bisa dukan ratar duniya, suka kewaye sansanin tsarkaka, dqa kamnatacen birni:wuta kuma ta sabko daga sama, ta cinye su." Ruya ta Yohanna 20:9.

**Yaya wannan mutuwan za ta kasance?**

"Wadannan,hukunci za su sha, madawamiyar hallaka daga fuskar Ubangiji da darajar ikonsa." 2 Tasalunikawa 1:9.

## *Gidan Fansassu (Cetattu)*

**Don wane dalili ne an halici duniya?**

"Gama hakanan Ubangiji ya fadi, shi wanda ya halici sammai; shi ne Allah; mai-sifanta duniya mai-yinta kuma; shi ya kafa ta, ya halice ta ba wofi ba, ya kamanta ta domin wurin zama: ni ne Ubangiji; babu wani kuma." Ishaya 45:18.

**Zuwa ga wanene Ubangiji ya bayas da duniyan?**

"Sammai na Ubangiji ne: amma ya bada duniya ga yan adam." Zabura 115:16.

**Don wane dalili ne an halice mutum?**

"Ka sanya shi shi yi mulki bisa ayukan hannuwanka; ka sa abu duka kalkashin sawayensa." Zabura 8:6.

**Da mutum ya rasa mallakansa, ga wanene ya bayar?**

"Gama shi wanda ya ci nasara bisa mutum, shi ke saka shi cikin bauta kuma." 2 Bitrus 2:19

**KA LURA**: Shaitan ya yi nasara da mutum a gonan Aidinin, don haka mutum ya mika mallakansa a hannun shaitan, wanda yayi nasara da shi.

**A lokacin jaraban Yesu, wane mallaka ne shaitan yayi kirarin cewa nasa ne?**

"Ya kai shi bisa, a cikin kyaptar ido ya gwada masa dukan mulkokin duniya. Shaitan ya ce masa, A gare ka ni bada wannan sarauta duka, da daukakarsu: gama ni am ba: dukan wanda na nufa kuma, sai im ba shi." Luka 4:5-6.

**Don me Yesu ya ce masu-albarka ne masu-tawali'u?**

"Masu albarka ne masu tawali'u: gama su za su gaji duniya." Matta 5:5.

**Menene Yohanna ya gani a cikin Ruya?**

"Na ga sabuwar sama da sabuwar duniya kuma: gama sama ta fari da duniya ta fari sun shude: teku kuma ba shi." Ruya ta Yohanna 21:1.

**Ko zasu samiu biyan bukata?**

"Za ya zama kuma, kamin su kira, in amsa: tun suna cikin maganakuma, in ji." Ishaya 65:24.

**Wane yanayi ne za ya kasance a sabuwar duniyan?**

"Kerkeci da dan-rago zasu yi kiwo tare, zaki kuma za ya ci chiyawa kamarsa: kura kwa za ta zama abincin maciji. Ba za su ciwutas, ba kwa za su yi barna cikin dukan dutse na mai-tsarki ba, in ji Ubangiji." Ishaya 65:25.

**Wadane lokutan sujada ne za a kiyaye a sabuwar duniya?**

"Gama, yadda sabobin sammai da sabuwar duniya, wadanda zan yi, za su dawama a gabana, in ji Ubangiji, hakanan kuma zuriyarku da sunanku zasu dawama. Za ya zama kuma, daga wani sabon wata zuwa wani, daga wata assabbat zuwa wata assabbat, dukan masu-rai zasu zo su yi sujada a gabana, in ji Ubangiji." Ishaya 66:22-23.

## *Sabuwar Urishalima*

**Yaya ne Yohanna ya dubi wannan Birni?**

"Na ga kuma birni mai-tsarki, sabuwar Urishalima tana sabkowa daga sama, daga wurin Allah, shiryayya kamar amarya da ado domin mijinta." Ruya 21:2.

**Tussa (fandishon) nawa ne birnin ke kafe akai?**

"Garun birnin kuma yana da tushe goma sha biyu, a bisansu kwa sunaye goma sha biyu, na manzanai goma sha biyu na Dan Rago." Ruya ta Yohanna 21:14.

**Menene ba za a yarda ya shiga birnin ba?**

"Ba kwa wani abu mara-tsarki da za ya shiga ko kadan, ko wanda ya ke aika kazamta ko karya: sai wadannan da an rubuta su cikin littafi rai na Dan Rago." Ruya ta Yohanna 21:27.

**Menene zaya dinga bulbulowa ta cikin birnin?**

"Ya nuna mani kogi ruwa na rai, maisheki kamar crystal, yana fitowa daga cikin kursiyin Allah da na Dan Rago." Ruya ta Yohanna 22:1.

**Menene yana sassa biyu na kogin?**

"A cikin sakiyar karabkassa. A wannan gefen kogi da wancan gefe kuma akwai itace na rai, mai-fidda yaya so goma sha biyu, kowane wata yana bada yayansa : ganyayen itacen kuma domin warkaswar al'ummai ne." Ruya ta Yohanna 22:2.

**Da me Yohanna ya ce an yi birnin da shi?**

"Karabkar birnin kuma zinariya ce sahihiya, sai ka che madubi garai." Ruya ta Yohanna 21:21.

**Don me yasa rana ko wata ba za ta kasance ba?**

"Birnin kuma ba ta da bukatar rana, ko wata, da zasu haskaka bisanta: gama daukakar Allah tana haskaka ta, Dan Rago kuma fitillata ne. al'ummai kuma zasu yi yawo cikin haskenta; sarakunan duniya kuma suna kawo darajarsu cikinta." Ruya ta Yohanna 21:23-24 (dubi Ruya ta Yoh. 22:5; Ishaya 60:19-20.

**Wadanne ne za a yarda masu su shiga cikin Birnin?**

"Masu albarka ne wadannan da ke kiyaye dokokinsa, domin su sami iko su zo wurin itacen rai, su shiga kuma ta kofofi cikin birni." Ruya ta Yoh. 22:14 (daga Juyin Sarki Yakubu. [KJV])

**"Baban hargitsi ya kawo ga karshe. Babu sauran zunubi, da masu zunubi. Dukan halitar Allah ta tsarkaka cikakken hadin kai. Za ya kasance a cikin dukan halitarsa. Daga wanda ya halici duka, ake samun rai, da haske da farinciki, da kuma cikin daukan sarari mara-iyaka. Daga halite mafi-kankanta zuwa duniya mafi-girma, dukan abubuwa, masu-rai da marasa-rai, a cikin kyaun su, da kuma cikakken farinciki, suna cewa 'Allah kamna ne'."** *great controversy page 678*